💫 _DISASTROUS LOVE_💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI_
_Wanan novel din na kudine is 500 naira, amman yanzu free pages nakeyi, so you can share and share and share, idan kinason ki shiga group din this novel send 500 to 3107021073 Aisha Muhammad first bank, saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461, Thank you Fanmily_

✍🏾M SHAKUR

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_

EPISODE1️⃣
_FREE PAGE_
Tsaye take cikin shagon kafen komputa, tana tsaye agaban kantan shagon tana sanye dawani dogon maroon hijab daya kode sosai yana jamata kasa tana kallon mutumin shagon wani dogon matashi dake zaune kan kujera gaban system yana danne danne a system din, daga gani kasan aiki yake aikin ma hala na yarinyar dake tsaye ne sabida yanda take kallonshi kaman tana hango abinda yakeyi akan system din. Zare manyan oily idanunta kawai take tana kallonshi gabanta nafaduwa tana fargaban karta fadi waec dinan bayan tasan da kyar Baba yabiya mata kudin tazana, batason abinda zaisa bazata shiga koda dan FCE bane, tana cikin dogon tunaninne taga Matashin mutumin yatashi dagakan kujeran dayake kai yay wajen printer dan daukan paper data bullo daga printer, cigaba da faduwa gabanta yayi tana kara zare idanun kaman kwan lantarki, daukan paper yayi yakoma table din yadau katin waec dinta yazo gaban kanta yamika mata takardan yana murmushi yace "congratulations Fatima Zarah an tsallake Waec kinada credit guda shida, 6 credit gareki natayaki murna, Allah ya sanyama takardan albarka" yay maganan yana mika mata takardan, karban takardan tayi da sauri tana kallon takardan tanada C a maths English da sauran important topic din dayakamata science student

nadashi, wani wani irin cool charming murmushi daya lobar da dimples dinta duka biyun tasake fararen hakoranta suka bayyana, batai wata wataba tawani irin zube akasa tai sujjada, dariya mai shagon yayi yajuya abunshi yakoma kujeran zaman shi yana dariya yace "wayaga su ustaziya Faty" tashi tayi tana murmushi tasauke yar jakanta da fatar jikin jakan dukta daye tsabagen wahala ta bude zip tasaka takardan da katin ciki sanan ta maida zip din ta zage sanan takalli mai shagon tace "nagode Yaya Habu" juyowa yayi ya kalleta ya kureta da ido ita bamata lurada kallon dayake mataba tajuya tafita daga shagon da saurinta tana tafiya takasa daina murmushi tsabagen yanda take murna kaman ba gobe, ahaka taketa tafiya ita kadai har zuwa anguwan su da yara suka cika layin suna wasa ana ihu ana wasa, wucewa tayi ta shiga cikin wani dan babban gida dakeda dogon zaure, gidan na hayane dake dauke da dakuna biyar, kowani daki falo ne sai uwar daka guda biyu, bayin gidan guda hudu biyu na wanka biyu na kashi General bayi, ga makwarara wajen wanke wanke ga dankararen kitchen dinsu inda kowa ke zuwa yay girkinshi, gidan yaci uban siminti kal kal kaman zaka taka ka zame.

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_

Babu kowa a tsakar gidan, ganin machine wayyo kudina agaban dakinsu yasa tagane Babanta na nan da sauri tai dakin nasu bayan ta gaida matan gidan datagani sun fito daga kitchen suka amsata ba yabo ba fallasa, sallama tayi ahankali ta shiga falon, falone mai dan kyau daidai, yaci ledan daki, ga kujeru masu kyau ga TV bango amman karami ga labule masu kyau da agogon bango bango dakin yaci fenti milk color, yarane adakin su hudu suna wasa, dan shekara sha biyu shine babban cikinsu mai suna Habib, sai mai binshi Ishak, saina ukun Bashir, ta hudu mace karama auta wacce dabo takeyi daga ganima ba'a yayeta ba mai suna Abida, yaran gasunan kai da kai kaman gwaranni farare kyawawa dasu, Babban cikinsu Habib dake sanye da kayan kanikawa ne ta kalla tace "Baba yadawo Habib?" gyadamata kai yayi yana tashi daga inda yake yace "eh yana daki shida Mamanmu" gyadamai kai tayi sanin idan Baba da Mama nadaki duk basa shiga ciki yasa tawuce dayan dakin dake facing dakin su Baba ta shiga katifa ce katuwar gaske akasa mai tudu takusan mmaye dakin  sai wata yagaggiyar katifa yar karama da aka jefa adan space din gefen dakin dayarage kusada inda ganamasgon kayansu yake, kan katifar taje ta zauna ahankali tana murmushi tasake ciro takardan waec din tana kallo shikenan itama zata shiga University kaman su Hafiza, idan Baba yafito zata gayamai yabata wayanshi takira Mami ta tasanar da ita.

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN

HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_

Tana zaune akan katifar taji muryan Maman su tafito tadauki Abida dake kuka tana lallashi sanan taji tana tambayarta. "ina Zakiyya kai Habib"? Kafinma Habib yabata amsa daga ciki sukaji muryan Baban su yana. "haba Habee nafa hanaki kiran yarinyar nan Zakiyya ki kirata da Fatiman ta, wani irin zakiyya yarinya nada suna mai kyau haka sunan diyar Annabi kina chanza mata" cikeda masifa tace "kai wlh Baban Habibu korafin ka bayi karewa kana daki kunenka na nan kana sauraron abinda mukeyi, yanzu dai me acikin suna dakake wanan bala'in da ranan nan" tai kwafa ta zauna tashiga bama Abida nono. Sanin zata sake kiranta yasa ta mike kawai tafito da saurinta tazo gabanta ta tsugunna cikeda girmamawa ahankali tace "gani Mama" harara ta watsa mata tace "kina ciki kina jina kikai shiru, saida ubanki yasa bakine sanan zaki fito mai halin munafukai, sai shegen yawo da hijabi kaman matar boka, oya ga Abida goyata kije kitchen akwai ruwa dana daura akan murhu ki hada ki kaima Baban ki bayi yaje yay wanka ki daura abincin rana" gyadamata kai tayi ta karbi Abida da zanin goyon ta datake mika mata, zata goyata kan hijabin ta daka mata tsawa tace "wai bazaki cire hijabin nan ki goya yarinyar nan ba kosaikin sakamin ita kuka nasamu tai shiru, autar Tawa zaki kashemin da zafi"? Batace komiba tacire hijabin ta ijiye sanan tajuya mata baya sabida kunya ta shiga goya Abida, binta da harara Mama tayi, shegun nonuwan nan dasuke nema sufi karfinta take boyemata yarinya kullum niki niki da hijabi, goyata tayi sanan tafice daga dakin tai hanyar kitchen itakuma Mama tajuya ta shiga ciki, ledan biredi ta dauko tafito tawurgama Habib tace "acici, shabiyu batayiba amman ka gudo daga wajen aiki kaman bakaci na safe ba, yaro saici uwa an aikoka duniya ne dankaitacin abinci, gashinan raba kaida kanninka ka kora da ruwa ka kama hanya ka koma aiki kadaiga sai yanzu zama adaura sanwa, ka kwashi su Ishak ka ijiyesu amakarantan allon malam idi" tai maganan tana watsamai harara yaron na turo mata baki yana kunkuni tawuce ta shiga dakinsu batare data karabi ta kansu ba.

Kwance wani magidanci yake akan gado wanda duka duka bazai wuce 45 to 50yrs ba yana lullube da zanin gado yadaura hannunshi abayan keyanshi yana kallon fankan dake kadawa ajikin silin din dakin, kana ganinshi kasan yayi nisa a tunani gyara labulen kofan tayi ta tsige dan zanin datake daure dashi tahau kan gadon tadaga zanin gadon ta shige takai hannunta kan joystick din ta taba jin ya kwanta yasa ta kalli fuskarshi, turo baki tayi saikuma ta shiga mannewa cikin jikinshi sabida tasamu ta tayardashi sucigaba, cikin dan fushi yatureta kaman jira yake yace "Haba Rukayya ke ina cikin babban matsala bakida damuwa, kinjefani cikin matsalan keko ajikinki, kawai kin kirani gida baki barni wajen nemana ba kawai nazo gida naita miki wanan abin uwa banda wani aikin yi" yay maganan cikeda dan takaici, yace "wai sabida kinga ina sonki saisa kikemin hakane Ruka? Miliyan uku fa Rukayya ina naga hanyar miliyan

uku yanzu iyye nanda sati daya zasu zo kuma, idan ban basu ba kinsan mizasuyi, kuma kekika turani naciyo bashin nan bakisa na tsinana komi dashi ba saidai kikasa nazo na kama wanan gidan hayan dayafi karfina, na saya miki kayan daki harda TV bango kikasa muka saya da fridge da katifun mu na daki yara da wanan rantamemen gadon dana siya miki kaman na amare, inda ace nai sana'a dashi da nasan inada at least wata hanyar biya amman bandashi kuma ko ajikinki, ke kawai daga safe har dare ki ganni manne dake kaman da tarayyan zamu biya bashi" cikeda kulewa tace "ya za'ayi kace ban damu da bashin da ake binka ba? Kanata wani cewa nasa ka kashemin kudin, naga aidai kaima kasai galleliyar machine wayyo kudina kana paparazzi akan titin gandujiyya, kai bakajin dadi yanda yan gidan nan suke bautamana mune yan uwan yan gayun gidan nan fa, yau taliya gobe farfesu, kullum ina jefar da ledan tsiren daka sayamin a tsakar gida suna gani, ga fridge ga TV, irin namasu kudin nan, kai bakaga yanda suke maula wajena ba, komi Maman Habib kai bakajin dadi? Babu abinda fa ba'a rokonmu, karka damu kudi zaizo zamu biya bashin sati daya ai akwai lokaci" cikeda fada yace "waini kika maida yaro Ruka? Tsafi zanyi dazan sami miliyan uku acikin kwana bakwai? Wai inama adashin dakika dinga karban kudin kina zubi kince min kwasa dubu dari biyu at least koshine nasamu nabasu wani abun" turo baki tayi tace "ni titini na kwasa nayi hidima da ita, nasoma yima Abida tari ne" wani kallo yamata yace "Abida ko Fateema"? Dauke kai tayi tace "nidai nasan kajini da kyau kakemin wanan tambayar Abida nace nafara ma tarin kayan daki, kana duba karkashin gadon nan zakaga abubuwan danasiya ma" wani irin kallonta yake saikuma yanisa yace "Abida dako shekara biyu batayi ba kokuma nace ko yayeta ba'ayibane kikema tari bama kiyi tunanin auren Fatima ba idan wani tsayayye yafito" dan gajeren tsaki taja tace "wanan batada farin jini har yanzu ko mashinshini batada shi, gwara Abida ma tun yanzu makota sun fara booking ma yaransu"

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_💫

DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

✍🏾M SHAKUR

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_

EPISODE2️⃣
_FREE PAGE_
Ganin yanda ya maida ita kaman  TV yana kallo yasa tacigaba tace "Inda kaga kayan dana saya dabakai korafi ba Baban Habib Mom Afreen Pre-order collection na shiga fa, nabiya kankanin kudi tayomana order gangariyan kaya tundaga kasan waje, wallahi bantaba ganin irin design din tukwanen da flask din dana sayaba har yanzu, wasu irin designs ne nadaban dan kayan danama Abida order babu irinsu agarin nan sai agidan masu kudi, ko masu kudin ma sai daidaiku, babu abinda zancema Maman Afreen sai Allah ya sakamata da alkhairi, gashi order kaya awajenta babu tsada, farashinta nada mugun rahusa kaga kaya kaman baka akayi kyauta, jira nakema wasu kudin su shigomana mukara yo order kaya daga kasan waje daga wajenta inyaso saimu bude shago ko Rabinraina mudinga saidawa" tunda tafara maganan kallonta kawai yake cikeda takaici matarnan tasashi amatsala Babba amman kuma ko ajikinta, ita batasan rigiman dasuke cikiba sai surutun banza takemai, abinda ke kara cimai rai yanda bai iya mata fada kaman an kullemai baki. Ganin yanda yake kallonta bayako kyaftawa idanunshi sun cikada hawaye sosai yasa sai jikinta yay mugun sanyi, ahankali tadaura kanta kan kirjinshi tana shafa kan nonon shi da hannunta tace "kayakuri Baban Habibu kaji, komi lokacine zaizo ya wuce kaman ba'a yiba, kudi zaizo In sha Allahu kaji zamu biya bashin nan kanka farau, ai ba'a kanka aka faraci ba, nidai kawai na hanaka karka sake kaje kana dako salon yan gidan nan sugano mekakeyi sudinga min gori, karka damu zan maka tunanin abu kaji" gyadamata kai kawai yayi sanan yadan tureta yatashi ya zauna yana mika hannu yana daukan jallabiya shi dake gefen gadon yasaka sanan yasauka daga kan gadon, dogone fari fat kana ganinshi kasan duka yaran falon nan dashi sukai kama, Maman cema baka, binshi da kallo tayi dudda taji haushin yanda baimata abinda takesoba amman saita share tace "muje naraka bayin daganan naduba yarinyar nan naga girkin" baice mata komiba Hijabi tadaura kan daurin kirjin dake jikinta

suka fito tare, matan gidan na tsakar gida tana fitowa tawani dagakai kaman bata gansu ba tabi bayanshi da sauri dan yamata nisa kanshi akasa bai masan ko akwai mata a tsakar gidan ba danshi baya kallon matan wasu yay hanyar bayi itakuma kawai sai tai kitchen koda ta shiga gani tayi Abida ma tayi bacci itakuma Fatima na fifita wutan wutan daya kama dan har sanwan ma natafasa bama tasan an shigo kitchen dinba sai fama takeda wutan idanunta sunyi jajir sabida hayaki, balla mata harara tayi tace "inkin gama ki fifita wutan kije ki kwantar da ita adaki" kai kawai ta gyadama Maman nasu dan batason tace wani abu takara kwafta mata zagi, juyawa tayi zata tafi saikuma kawai tai tsaki tazo ta bayanta tace "bani y'ata" takai hannunta zuwa saman kirjinta zata kwance zanin runtse idanunta tayi amugun firgice hakan yasa Mama ta tsaya tana kallonta da mugun ban haushi saikuma ta dakamata tsawa tace "dalla kwantomin y'ata kina rurrufe idanu kaman mai surkulle" har wani ajiyan zuciya ta sauke tace "uhn to" sanan ta kwance Mama ta karbeta suka fita itakuma tacigaba da girkin.

_MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP, SHAHARAREN GROUP NE DASUKA KWARE KAN HARKAN ORDER, IMPORTATION DIN KAYA DAGA KASASHE DABAN DABAN NA DUNIYA AKAN KUDI DAN CINGILI, INDAI A MOM AFREEN PRE-ORDER GROUP NE KARKAI FARGABAN YIN ORDER DA ITA DAN AIKINTA NE, TA KWARE A BANGAREN TANA HARKA DA AGENT DABAN DABAN DAGA KASASHE DABAN DABAN, ZAKU IYA TUNTUBARTA AWANAN NUMBER 08069493528, DAZARAN KUNYI SAVING ZAKU GANTA A WATSAPP KUMATA MAGANA, KARKU BARI WANAN GARABASAR TA WUCEKU_

Wuraren 3 tagama girkin tadauki tukunyar a wata tray tafito tai dakinsu dashi Babansu tasamu zaune kan kujera yana rikeda remote Mama zaune gefenshi da alamu abincin duk suke jira tana ganin Babanta tasake sakin murmushi da kana ganinta kasan daga zuciyanta yake, harara Mama ta watsa mata tace "Malama ajiye tukunyar ki kwaso kwano na zubama Baban ki" da sauri Baba ya watsa mata mugun kallo yace "bazaki bar yarinya ta hutaba" ya kalli Habib daya shigo yayi kini kini da rai sabida yunwa yace "wuce ka kwaso kwanuka azuba abinci" da sauri Mama tace "wai sai insa abu kanuna agaban yara ban isaba" ahankali Baba ta hanyar rage murya yace "tagaji ne tahuta, tanada kannai intai girki sai asaka kannan suyi wani abu ko" Mama zata kara magana ya kalli Fatima datake tsaye inda take kanta akasa sai zufa take yace "Zahra'un Baba ya jarabawan andubo"? Da sauri tadagamai kai tana murmushi tana kallonshi kana ganin yanda take kasan yarinyar na mugun son mahaifinta, shima murmushi ya sakin mata cikeda sonta yace "dauko takardan nagani" da sauri tai uwar dakin su Mama tabi bayanta da harara daidai lokacin Habib yakawo plates karba tayi ta zuzzuba musu abinci tazuba na Fatima kadan ta ijiye agefe har Baba zaiyi magana saikuma yayi shiru kawai baice mata komiba, yadau nashi yasa cokali ya shiga ci murmushi kawai yayi shi kanshi yana alfahari da Fatima wajen girki danko Ruka bazata nunama yar karaman yarinyar nan yanda ake girki ba. Fitowa tayi daga dakin hakan yasa tun kafin ma takaraso ya ijiye abincin shi agefe yamika mata hannu tasamai takardan wajen kafanshi yanuna mata yace "zauna ga abincin chan dauko kici" kallon abincin tayi saikuma ta kalli na kannenta ba tace komiba Allah ma ya taimaketa batada wani cin hauka data mutu da yunwa, daukowa tayi tazo ta zauna kusada mahaifinta shikuma yana duba takardan murmushi kawai yayi ya gyadakai yace "uhmm Masha Allah wanda baida

Fatima baida mene....." dan murmushi tayi murya chan kasa mai shegen zaki tace "sa'a" bata fada da karfi ba sabida mamansu, murmushi Baban yasakeyi ya kalli Maman su yace "yarmu tacinye waec tass" sanan ya kalli Habib dake kallon takardan yanacin abincin yace "kagani haka nakeso kaima kadinga kokari a makaranta kaine namijin gidan nan, babanmu amman kullum na bayan kashi kake, abu daya kawai ka iya shine son abinci" daure fuska tamau yayi baice komiba Baba yataba kan Fatima dakecin abinci tana murmushi yace "yanzu sai kwaleji ko Zara'un Baba, lawyer gidan nan, Allah shi albarka, Allah ya sanya ma certificate din albarka yanzu dazaran wani tsayayye yafito sai aure ko" wani irin kunya ne yakamata da sauri ta tashi tadau abincin ta tai dakinsu, kyalkyacewa da dariya Baba yayi Habib natayashi, Baba ya girgiza kai kawai, tabe baki Mama tayi tace "yartaka da Batada mashinshini gwarama kadena tunanin aurenta yanzu dan ko almajiri batada shi ballema mutumin arziki" sosai maganan ya sosama Baba rai hakan yasa yace "aure lokaci ne Rukayya, yana zuwa akeyi kodako kana coma ne, dududu ma shekarun nata nawane? Ko ashirin bataiba dan haka kisha kurumin ki mijin Zara'una na nan tafe ko Habibun Babanshi" da sauri Habib ya gyadama Baba kai yana murmushi yace "eh Baba wlh inaso inga muma munyi biki kaman gidansu Mansur yayar su tai aure, nima inaso Ya Faty tai aure" murmushi Baba yayi yakai abincin shi baki yana saurararan labarin da Habib ke basu na bikin yayar abokin shi. Saida yagama tsaf sanan yatashi yakalli Mama dake bama Abida data tashi nono yace "bari nafita nema saina dawo" yataba kafan Abida dakeshan nono yace "Yan Matan Baban ta yauko kallona ba'ayi sabida an sami Mama" ture hanunshi tayi dagakan kafanta dan bata kaunar abinda zau hanata shan nonon nan, dan dariya yayi yace "au abun na fadane, zanga mai kawo miki cizi anjima kiyita shan nonon ki" ya kalli Mama yace "natafi" cikeda kuncin rai Mama tace "a dawo lpy" fita yayi rikeda takardan a hannunshi yana gungura machine dinshi ya kwalamata kira. "Zara'u" daga daki ta amsa "na'am Baba" cigaba da gungura machine dinshi yayi zuwa zaure, fitowa tayi sanye da hijabi kanta akasa tawuce tafita daga falon tai hanyar zaure Baba tagani haryay parking machine din awaje ya shigo zauren murmushi yamata yamika mata takardan waec din yace "Allah yamaki albarka yabaki miji nagari kinji, wanda zai soki sanan yakula dake sama dani, kome ake miki kicigaba da hakuri dudda nasan ke yarinya ce mai hakuri ga kunya, ga kawaici wata rana sai labari kinji" gyadamai kai tayi ahankali, ahankali yace "kin koshi da abincin data zuba miki"? da sauri ta gyadamai kai tace "nakoshi wlh Baba" shiru yayi yana kallonta kaman wanda yake wani tunani ganin yanda yake kallonta yasa saitaji tadamu tace "Allah Baba nakoshi kasan banamaka karya ko" sosai idanunshi sukai ja yace "nasani Zahra, bakimin karya na shaidake da wanan y'ata" hannunshi yatura a aljihu yaciro last 1k dayake da ita, mika mata yayi yace "gashi ki boye kidinga kashewa ahankali, kome kikeso ki dinga siya kinji yanzu banda kati awaya, nadawo zan loda kati saina baki ki kira Babarki ki fadamata sakamakon waec dinki kinji" karban kudin tayi tareda dan dukawa tace "nagode Baba Allah ya saka da alkhairi yakara budi" sosai idanunshi sukai jajir yace "wuce kitafi hudu nayi ki tattara kanninki kuwuce islamiyya kinji, ki dage dakaratu ilimi shine adon y'a mace" gyadamai kai tayi tace "Tom Baba" kanta yashafa da hannunshi yadan rungumota side dinshi yace "kiyi addu'a Allah bama babanki kudi, zan sayamiki waya tunda kema yanzu kin dawo budurwa kaman kowace budurwa, da sababbin zannuwan da takalma kinji, da kayan kwalliya" murmushi tayi akunyace tace "Baba karka damu komi lokacine, Allah ya azurtaka da arziki na halas katafi karkai latti" tai maganan tareda juyawa da sauri batason ta nunamai kalamanshi sun tabata, tsayawa yayi shima yabita da kallo harta shige ciki,

maganan da Ruka tamai dazu ya sosamai rai ba kadanba kuma deep down yasan da gaskene Zara batada ko mashinshini guda, kuma laifinshi ne yarinya batada kayan arziki tana mace kuma budurwa datake tasawa yanzu amman kayanta sunfi name abincin saidawa kodewa, hijaban ta biyu kacal da maroon dawani mai ruwan toka sun kode harsun fara ja akai tsabagen kodewa, batada wani takalmi na fita sai silifas, kullum fuskarnan nata fayau babu komi aciki yaza'ayi saurayi zai gani ya yaba, koya sami kudi yace zai mata Ruka tahana, saisa yakeson yarinya yanzu ta shirya taje wajen Babarta hutu amman yasan Ruka bazata bariba, ganin dogon tunanin dayake yasa kanshi yafar*a sarawa yasa yajuya yafita kar hawan jininshi yatashi, machine yatada yafice daga anguwan gabaki daya

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&G_

✍🏾 M SHAKUR

EPISODE3️⃣
_FREE PAGE_
Koda takoma daki bataga Maman nasuba hakan yasa ta shiga dakinta ta ijiye komi taboye kudin da Baba yabata sanan tafito tatattare falon inda sukaci abinci ta share tafita da kwanukan

ta wanke sanan tadawo ta kunna turaren tsinke afalon ganin ana kiran la'asar yasa tadauro alwala ta shigo tai salla sanan ta shiga dakinta ta sanya Ash color hijabin ta har kasa dan shine na islamiyyan su sanan tadauki jakar islamiyyan tafito, gaban dakin Maman su taje ta tsaya tai sallama ahankali, daga ciki maman tace "lafiya kin isheni da sallama yarinya saikace rainon mayu" batadamu da maganar ba dan inda sabo tasaba, ahankali tace "zantafi islamiyya ne Mama natafi"? Ihu tamata daga taciki tace "au so kike ubanki yazo yace nahanaki zuwa islamiyya ko uwar shairi da kinibibi wuce ki bacemin daga gaban daki, mayya mai neman rabani da mijina" juyawa tayi ahankali tafice tai waje da sauri sauri take tafiya kaman mai jiran wata, tayi nisa sosai tahango wata yarinya kana ganinsu kaga sa'oinnin juna itama tana sanye da Ash color hijabin kaman nata tana tsaye karkashin bishiya tun kafin takaraso wajen tace "wlh kika samu latti Fatima saina rama dukan lattin da za'a min ajikinki" dan dariya tayi ta bangaje mata kafada tace "dalla chan bamuyi latti ba har yanzu hudu bata cikaba" binta da sauri yarinyar tayi tace "au hakama zakice"? Murguda mata baki tayi tace "eh din" dariya yarinyar tayi tace "tokijirani sai sauri kike FatynBaba" juyowa tayi ta tsaya chak tareda rike waist dinta tace "ohkay ke Maryam dinan kin cika wayau, sabida muyi lattin kirama dukan ajikina ko saisa kike cewa najiraki" dariya Maryam tayi takaraso inda take tareda mika mata wani leda tace "gashi nakine" da sauri ta karba tabude taga sabon hijabin islamiyyan sune Ash wanan ma anyi dinkin mai hula mai kyau juyowa tayi ahankali ta kalli Maryam din dake kallonta, murmushi tayi ta bangaje mata kafada tace "ke dalla common, Babanmu nacema hijaban mu na Islamiyya sun tsufa, shine yace nazo shago anjima a aunani a dinka mana, shine naje kinsan yanada yadin hijabai masu kyau, na zaba yabama yaron shagonshi ya dinka mana dinki daya, nima bansa nawa bane sabida nasan bazaki saka naki yauba, sai gobe zamu saka mu fasa islamiyyan tareko" gyadama Maryam dinkai tayi saikuma ta rungumeta kawai, da sauri Maryam ta tureta tace "dalla ke dadina dake son jiki awaje zaki wani rungumeni sabida hijabi, har yanzu maganana nanan kikasa mukai latti saina rama dukan ajikinki" Maryam tai maganana tana dariya taredayin gaba, share hawayenta tayi ahankali sanan tabi Maryam din da sauri tace "toni kijirani" haka suka dinga tafiya suna shirme cikin ikon Allah koda sukakai ba'a fara taron latti ba hakan yasa suka wuce ajinsu direct aka fara karatu.

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&G_

Karfe shida aka tashesu daga islamiyan, saidaa ta tattaro kansu Sadiq dasuka taho tareda Habib sanan suka fito Habib yay gaba da kannin nashi itakuma suna jerowa tareda Maryam suna hira har sukakai wajen bishiya suka tsaya Maryam tace "kinga yanda Malam Sani keta

kallonki kuwa dakike biyamai karatu" dan hararanta tayi tace "kallo, kallon lafiya, ni banmasan anyi hakaba kin iya sa ido Maryam" murmushi kawai Maryam tayi tace "nidai kidinga saka nikabi, kyanki yay yawa yarnan" hannu takai zata kwadama Maryam din duka ta kwashe aguje tadau hanyar layinsu itakuma tacigaba da tafiya tana dan murmushi, ana magrib suka shiga gida, gaida mutanen gidansu tayi sanan tai dakinsu Mama tasamu afalo zaune tana bama Abida nono tana ganinta tace "wuce kije ki kada miyan dake wuta" dakinsu ta shiga ta cire hijabin islamiyyan ta tasaka maroon tafito zatai kitchen, da sauri Mama tamata ihu. "sokike kije ki kone a kitchen Babanki yakusa cinyeni, wuce dan ubanki kicire hijabin nan bansan ubanwa kike boyema yan kirgan dangin nan dakika faraba" cikin kunan rai Habib yace "waike Mama kullum saikin ma Ya Faty fada dawani wai kirgan dangi mehaka dan Allah, ni wlh kidena damun Ya Faty" cikin fushi ya kalli Fatima da kanta kekasa yace "Ya Faty jekiyi da hijabin ki kinji ai Malam yace bakyau mace na yawo haka ba lullubi" mugun dundu Mama takaimai abaya tace "kai dan ubanka ko ubanka bayaja da maganata balle kai yaushe aka haifeka? Duka duka shekarunka sha biyu kake gayamin magana eh dan ubanka" cikin kuka da fushi yace "to meta......" da sauri Fatyma tajawoshi taredakai hannu bakinshi ta taushe tahanashi magana dan Allah ya zuba mata son kanninta kaman me, cikin fushi Mama ta ijiye Abida kan kujeran ta tashi tace "ni uwarka kakema rashin kunya kan wanan yarinyar eh Habibu" da sauri Faty ta tura Habib din bayanta tace "kiyakuri Mama dan Allah" gauramata mahaukacin mari Mama tayi da saida yasa tai layi kaman zata fadi sanan ta fizgota da karfi ta kumata da bango tareda shake mata wuya tace "ni zaki juyawa yarana akaina? Yaran dana haifa zaki batamin su? Harda kama Habib kina boyewa a bayanki irin ga danki dinan ke uwarshi wlh yauna lahira saiya fikijin dadi" tai maganan tareda fizgo wayan TV tashiga lafta mata tun tana daurewa bata ihu tahau kuka sosai tana ihu tana yakuri Mama, Habib na tsaye gefe yana kuka sosai kaman ranshi zai fita, duka yaran harda Abida ma saisuka hau kuka ganin ana dukan yayansu ga Mama sai uban ihu take tana jibgarta kaman daman tana tikeda ita, wata makociyarsu ce dake shiri da Maman tashigo tana zuwa rike Mama tayi tace "ya isa hakanan Maman Habib" cikin kumfan baki tace "barni na kashe yarinyar nan nahuta Zainabu, yarinya tarabani da mijina, mijina saiya hanani kudi yabama wanan makiran, komi ita komi ita, yanzu kuma nema take tarabani da yarana, to wlh bata isaba saina kasheta nakashe banza taga idan da abinda ubanta zai iya yayi kuma zama daram sai yanda nayi da uban nata datake takama take tunkaho dashi" tai maganan tana haki sosai kaman zuciyanta zai fito baki, kallon Fatima dake duke tana kuka sosai tayi kanta akan guiwanta tace "kekuma tashi kibar nan kije kiyi girkin, kafin natayata kara miki algunguma mai kama da larabawan jahannama" ahankali tashiga tattaba bango tamike tsaye da kyar jikinta har kyarma yake tsabagen wayan wutan datasha sanan tawuce ta lallaba tafita daga dakin tai kitchen, saida tafita sanan matar tace "kiyakuri kedai kiyita addu'a Allah bata miji ta tattara tabar miki gidan nan ki sakata ki walada mijinki" da sauri tace "ina Allah yabata, yarinya sai bakin jini gadon uwarta, ko mashinshini batada shi" da sauri matar tace "duk kyan nan nata" da sauri Maman Habib tace "kyan dan maciji ne, tayi gadon bakin hali ina zata samu wanda zai kwasheta yakaita gidanshi amatsayin mata"? "adai dinga hakuri Maman Habibu amman dai ina bayanki kitashi tsaye karki bari tabata miki yara" murmushi tayi tace "nagode Maman Zainab, bari ta sauke abinci zan aiko miki dashi, wlh nagaji dacin shinkafa taliya kullum yau kawai nai marmarin tuwon shinkafa da miyan taushe da kan rago zai aiko miki dashi nariga nagama miyar" cikeda jin dadi har wani sude baki Maman Zainab take tace "Allah bar mana Maman

Habibu kap gidan nan babu kaman ki, godiya nake, bari naje to", fita tayi tana karamata godiya, itakuma Mama ta kalli Habib dake kuka har lokacin tace "zonan" zuwa yayi yazauna agabanta shafa kanshi tayi tace "kaga kasa nadakeka a banza ina ruwanka da wanan shegiyar nace muku ba yar uwarku bace, ya isa dena kukan jedaki kadauko biredin dana ijiye muku kaci kaida kanninka" ko kallonta baiyiba yatashi ya shige dakinsu fuuuu, tabe baki tayi tadauki Abida tace "mayyar nono ungo kafin ki kashemin dodon kunne" .

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&G_

Taci kuka harta godema Allah sanan tai shiru, babu indabaya mata ciwo ajikinta haka adaddafe ta kada miyan ta kashe wutan tadaura miyan atray tadauka tana tafiya ahankali tawuce daki, har gaban Maman takai tukunyar ta ijiye ahankali murya chan kasa tace "Mama gashinan nagama" ko kallonta Maman batayiba hakan yasa ta dafa kujera tamike tsaye da kyar zata wuce dakinsu Mama tace "ubankine zai dawo daga wajen neman dayaje yakawo miki kwanukan daza'a zuba abincin"? Girgiza kai tayi tawuce takwaso kwanukan da Mama tazuba tuwon already, miya Mama ta zuzzuba ta mikama yaran sanan tadau kwanonta ta zuba miya kafin tadau kwanon ta wurga mata da tuwon da miyan suka bare kan hijabin ta ihu tayi sosai dan yadan tabamata jiki ta tashi tacire hijabin tana kuka sosai, hararan ta Mama tayi tace "bacemin daga gani jaka kawai mai bakin jini" dakinsu tawuce ta shiga ta ijiye hijabin awaje daya ta kwanta akan gadonta jikinta na kyarma har lokacin tana kuka ahankali, Habib najinta amman yakasa cemata komi but bakaramin tausayinta yakeji ba, tayi kuka tayi kuka ahaka bacci yay gaba da ita batai magrib ba balle ma isha'i.

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&G_

Wuraren goma da rabi baba yashigo lokacin duka yaran sunyi bacci lekasu yayi ganin duk suna bacci yasa yasaki labulen yawuce dakinsu zaune yaga Mama tana kullama Abida datai bacci pampers yace "kowa yaci abinci ko Ruka" fuska adaure tace "jeka tashesu katambaye su mana" murmushi yayi yace yau yan rigiman na nanne, kulanshi yaja yashiga cin abinci batare daya karace mata komiba saida yagama sanan yay yan abubuwa kafin yarage kayan jikinshi ya

kashe wuta yazo yahau gadon ya kwanta yay shiru, juyowa tayi ahankali tace "kasamo wani abu?" girgiza mata kai yayi yace "duk wayanda nake tunani zasu iya bani bashin kudi basu baniba, lokaci na gudu Ruka ya zamuyi bakiji yanda kaina keciwo ba wallahi" tabe baki tayi tace "karkaje kajama kanka jininka ya buga abanza duk yanda kaddara tasamu mutum haka yake daukanta" shiru dukansu sukayi basu sake cewa komib*a kowa da abinda yake tunani aranshi......

_DAN MAGANA DANI M SHAKUR KOKUMA KARIN BAYANI KAN ADVERT A TUNTUBENI ANAN 07012181461_

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&GNaturals_

✍🏾 M SHAKUR

EPISODE4️⃣

_FREE PAGE_
Wuraren karfe uku wani mugun azababben ciwon ciki yatadata, da farko tazaci mafarki take amman sai taga ba mafarki bane, wani irin murda wa da cikinta da maranta sukeyi kaman ana murda hanjinta kanta na shegen sarawa, kokarin tashi tayi daga kwancen datake amman takasa sabida komi najikinta wani irin ciwo yake mata, ahankali tasaki wani wahalallan kuka mara sauti..... cikin bacci kaman daga sama Habib yaji sheshekan kuka tashi yayi yabude idanunshi, dayake yanada wata yar karaman tocula hakan yasa ya kunna ya haska Fatima dake kwance idanunta sun kumbura sunyi jajir sabida kukan datasha jiyada daddare gakuma bacci, karasawa yayi kan katifarta da sauri, murya chan kasa gudun kar Mama tajisu yace "Ya Faty menene kike kuka"? Yay maganan yana kai hannunshi saman goshinta wani irin zafi dayaji yasa da sauri yadauke hannunshi yace "innalillahi Ya Faty bakida lpy in tada Baba"? Girgizamai kai tayi, cikin muryanta da ba'aji sosai tace "dagani na zauna" hannunta datake mikamai yakama yadagata ta zauna da kyar tana share hawaye tana cizan baki, sosai yaji tabashi tausayi, yanason Ya Faty kaman ba gobe dan tamafi kulada su kan uwarda tahaifesu, tun suna yara itane komi nasu, duk in yanajin yunwa saidai in Ya  Faty batada kudi amman saita bashi yaje yasai wani abin, idan basuda lpy, Mama nafita kome sukeso saita dafa musu suna gamawa su wanke tukunya ta yanda Mama bazata saniba, ganin yanda hawaye yakasa dena zuba daga idanunta yasa yakoma kusada ita ya zauna kanshi ya daura kan hannunta yafashe da kuka ahankali gudun kar ajisu murya chan kasa yace "Ya Faty kiyakuri kinji Allah na sama yana kallo wata rana sai labari, Mama batada kirki kuma batason ki amman kinga duk ranan dana girma zan daukeki daga gidan nan nasai miki wani gida nasai miki mota nasa police nace musu karsu bari Mama ta shigo balle ta dakeki kota saki kuka, I promise idan na girma ko maganan banza babu wanda ya isa yafada miki kinji, kidena kuka, bari na girma kiga abinda zai faru kidena kuka" yay maganan yana share hawayen dake zubomata, danne kukan tayi takai hannunta ta sharemai hawayen shi shima tana murmushi tace "ninasan kanina soja ne, Habib dina, nasan idan Habib ya girma ko kallon banza babu wanda ya isa yamin, Habib dina sojana toko tubambale mayen abinci" dariya yahauyi kaman bashine ke kukaba, murmushi tamai tace "jeka koma baccin ka kaji" da sauri yace "kinji sauki"? Gyadamai kai tayi alamun eh, tashi yayi yawuce ya kwanta awajen shi yace "dazaran yacigaba ki kirani kinji" Tom ta amsashi ahankali, kwanciya yayi tareda kashe toculan, sai alokacin taji ashema hiranshi rahama ne agareta wani mahaukacin ciwone yakamata dayasa taji kaman zata kurma ihu amman ta daure tarasa inda zata saka kanta taji dadi, har aka kira asubahi idanunta biyu, har aka tashi tanaji Baba yabude kofa yafita yadawo amman takasa koda motsi.
**

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&G_

Wuraren shida nasafe Habib yaji wani irin nishi da sauri yabude ido ganin gari yay haske yasa ya kalli katifar ta da sauri ganin Ya Faty kwance tana wani irin nishi kaman wacce ake fizgema numfashi yasa yawani irin kwala ihu. "Ya Faty!!!" yatashi da gudu yay kanta, ganin jini akan gadonta yabaci jikinta yabaci Ya Faty dabaka ganinta babu hijabi amman wanan karin zaninta wuri guda, yar under skirt dinta baki iya cinyan ta ne kadai yarage ga fararen cinyoyinta sun baci da blood yasa Habib ya kwalama Mama kira. "Mama! Mama! Baba! Babaaa!!" dawani irin sauri Abba yadiro daga gado dagashi har Maman suka fito jin yanda Habib ke kwala musu kira, Abba ne yariga shigo dakin Mama biyeda shi, kafinma Abba yay magana ganin Fatima yasa yay kanta da sauri yace "innalillahi wa innailaihi raji'un, maiya sameta Habib? Ke Zara'u, Zara'una Baba"? Gabaki dayama batasan inda kanta yakeba daukanta Baba yayi yasata ajikinshi yana jijjigata yace "ke Zara'u, kallen, nine nine meke damunki"? Cikin kuka Habib yace "tun cikin dare naji kukanta, jikinta yay zafi tahanani tadaku ni bansan meke mata ciwo ba" dagokai da sauri Baba yayi ya kalli Ruka dake tsaye inda take yace "Ruka huramin wuta kisa ruwa tai wanka mutafi asibiti" hararan shi tayi tace "ai hala kasayo itace ne" da sauri yace "to saman mini awajen makota dan Allah" tsaki tayi tace "kaima kasan abinda banyi kenan rokon makota saidai ni suzo suyi maula wajena, Um ni kaga tafiyata ku karata" tawuce tasakin musu labule tai gaba abinta,  rasama abinda zaiyi yayi ganin haka yasa Habib yace "bari naje wajen Maman dadi" "yauwa Habib" da sauri Habib yatashi yafita bucket yadauka yay kitchen din gidansu wajen wata mata dake kitchen yaje direct cikeda tashin hankali yace "Maman Dady dan Allah ki tsammana ruwa Ya Faty batada lpy wanka zatayi mutafi asibiti" da sauri Maman Dady tazuba mai aroba tace "ayyah Allah bata lpy" karban ruwan zafin yayi yaje bakin rijiya ya sirka ruwan yadauka yakai bayi sanan yadawo daki, lokacin daya shigo yaga har lokacin tana jikin Baba daidai tabude ido, ahankali Baba yace "meke miki ciwo Zara'u"? Murya chan kasa tace "ciki da kai" Habib daya tsaya kansu yace "Baba nakai ruwan bayi" ahankali Baba yace "zaki iya tashi tsaye ki chanza kaya"? Gyadamai kai tayi tashiga kokarin tashi da taimakon Baba da Habib tamike tsaye, zani Baba yanemo mata yasamata a hannu yace "cire kayan ki daura wanan saiki kirani zomu fita mubata wuri Habib" fita sukayi shida Habib dakin Mama ya shiga yasame ta zaune tana bama Abida nono, cikeda damuwa yace "dan Allah zoki taimakawa yarinyar nan tai wanka kinga suma taketayi Ruka" wani kallo tamai tace "gaskiya kayakuri amman bazan iyaba kuje chan ku karata" jin karan fadin abu timm yasa dagudu daga Baba har Habib sukai dakin itane tazube akasa asume tacire kayan amman bata gama daura zanin da kyau bama. "innalillahi wa innailaihi raji'un kawomin ruwa Habibu" Baba yay maganan yana daukanta yana gyaramata daurin zanin tareda fitoda ita falo, daidai Habib nakawo ruwa, shafa mata a fuska yayi ta farfado kaman zai mata kuka yace "sannu kinji, Habib biyoni da soson wanka" tama kasa tafiya daukanta Baba yayi har zuwa bakin bayi yama rude yarasa yanda zaiyi kallonta yayi yace "zaki iya wanka"? Gyadamai kai tayi idanunta dabasa buduwa da  kyau, da sauri Habib yace "Baba wlh bazata iyaba kartaje tafadi tasume abayi" hayaniyan su da Maman Dady taji yasa tafito daga kitchen ta zagayo hakanan tanason Fatima sabida natsuwa da kunya da girmama na gaba da ita, tana kallon jikin mahaifinta yanda yabaci da jini tagane meke damunta tace "assha sannu Fateema, kawota nan Baban Habib bari natayaku" da sauri Baba yamika mata Fatyma, karbanta tayi ta shigar da ita bayi babu ko karfi daya ajikinta, sanan ta

turo kofan tsayawa Baba da Habib sukayi suna jiransu, basu wani dadeba Maman Dady tafito da ita tace "dauketa Baban Habib zata iya zubewa Allah yasawake" da sauri Baba yadauketa yace "nagode Allah ya sakada alkhairi" wucewa da ita Baba yayi shikuma Habib yadauki bucket da so so Maman Dady tabisu da kallo bakaramin tausayin Fatyma takeji ba, daga ita har Mahaifin nata da aka gamada shi, bata shiga harkan Maman su sabida wlh zata iya mata dukan tsiya kan fatyma dan arayuwanta ta tsani zalunci, tadade tana tunani saikuma kawai tawuce ta shiga dakinta, always ta dauko tasaka a leda dawasu sababbin pant da mijinta yasayo mata na jegon Dady dabatai amfani dasuba dan sunmata kadan, kullewa tayi a bakar leda, sanan tafito tai sallama gaban dakinsu fitowa Habib yayi bashi tayi tace "gashi kabama Baban ka yabama Fatima" karba yayi yakoma  ciki itakuma tawuce abinta.

Baba na kokarin zaunar da ita kan gadonsu Habib, Habib ya shigo ya mikamai ledan da Maman Dady tabashi tace "Maman Dady tace kabama Ya Faty" karba Baba yayi yabude ganin me aciki yasa yabata yace "kin iya amfani dashi Zara'u"? Gyadamai kai tayi idanunta na kukkullewa dan bata gani sosai, barinta Baba yayi akan gado yaje wajen kayanta yadauko mata wani atampan na riga da zani bakida da ruwan toka sanan yadau sabon hijabin da Maryam tabata dayagani saman kayanta ya ijiye mata komi gefenta yace "lallaba ki  saka kayan kinji bari nahado miki shayi nazo" fita sukayi shida Habib yawuce uwardakan su ko kallon Ruka baiyiba yay wajen kayan shayi yadeba yazuba a kofi sanan yazuba ruwa ya yagi buredi yafito tsayawa abakin kofan yayi yace "kin gama Zara? Zara" yasake kiranta shirun dayaji yasa ya kutsakai ya shiga dakin ganinta yayi tasa pant din da pad ajikinta, tasaka riga amman takasa jan zip din ta kwanta akan gadon tana wani irin rawan sanyi kaman wacce zata mutu, rasama mezaiyi Baba yayi yace "innalillahi Zara'u karkimin haka kinji" dagata yayi jikinta kaman wuta yahada zip din yaja sanan yadau zanin dagakan gado ya daura mata sanan yazauna akan gado yana kwalama Habib dake falo kira. "kawomin shayin Habib" shigowa Habib yayi da shayin ya karba yace "sha tea kadan kidan samu karfi saimu tafi asibiti ko" girgiza mai kai tayi tareda sakinmai kuka ahankali da muryanta dabaya fita tace "Baba ni kasayo min magani allura za'amin a asibiti" murmushi yamata yace "sha shayin to mugani tukunna inkinsha da kyau sai na sayo miki magani" kai shayin bakinta yayi ta kurbi kadan ko idasa hadiyeshi bataiba sai amai bata kasan dakin tayi da aman da babu abinci aciki, tashi Baba yayi yace "bari na chanza kaya mutafi zauna da ita Habib" zama kusada ita Habib yayi yadau hijabinta yasaka mata shi karan kanshi saida tace "kai wanan hibajin mai hulan nan yamiki kyau sosai" daki Baba ya shiga ya chanza kaya yadau key machine dinshi sanan yajuyo ya kalli Mama yace "bari nakaita asibiti" yan dubu biyun dake aljihun wandon shi yaciro yakalla sanan yatura a aljihu sanan yawuce yafita ya gungura machine dinshi zuwa waje lokacin 8 dayan mintoci nasafe sanan yadawo ciki, dagata yayi Habib yakawo mata silifas dinta tasaka Baba yariketa tana ta karkarwa da kyar suka fita waje saida yafara daurata kan machine din sanan yahau yatada suka tafi General.

Ahankali yake gudu da ita jin yanda jikinta ke bari, saisa sukai kusan 30min kafin sukai, parking yayi inda ake parking ya sauko ahankali sanan yakamata ya saukoda ita yana tattare ta gudun karta fadi yace "sannu Zara'una, muje" riketa yayi suna tafiya ahankali tana binshi ahankali dishi dishi take ganin gabanta daidai sun shiga ciki dip tadena ganin komi daga sama sama taji

muryan Babanta na ihu "ataimakamin ataimakamin jama'a".

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&GNaturals_

Dawani irin gudu nurses suka gungunro wani gado aka karbeta daga hannun Baba suka dagata sauka daurata akan gadon akai ciki da ita, wani babban examination room suka shiga da ita Baba zai bisu aka hanashi shiga sanan daya daga cikin nurses din tafito tashiga wani consultation room saigata tafito tareda wani Dr dabazai wuce 35yrs ba yana sanye da farin glasses a idanunshi wuyanshi sanye da stethoscope, wajen aljihun Lab coat dinshi ta gaban rigan anrubuta Dr Imam, da sauri sauri gudu gudu suke tafiya daidai zasu shiga dakin Baba yarike hannunshi gam hakan yasa yajuyo tareda tsayawa ya kalli Baba yakuma kalli hannunshi da Baba yarike irin lafiya, kaman wanda yazare dakin Baba yanuna mishi cikin wata irin raunanniyar murya yace "likita y'ata ce acikin dakin, dan Allah kataimaka mata kar wani abu ya saman mini Zara'una likita" wani calm smile Dr yayi tareda karbe hannunshi daga hannun Baba yakama kafadar Baba ya zaunar da Baba kan kujeran dake wajen yace "abinda nakeso dakai Baba shine ka kwantar da hankalin ka kazauna anan kama yarka addu'a, abangarena kuma namaka alkawari zanyi duk abinda zan iya naga na ceto rayuw........." bai karasa maganan ba wata nurse tafito tace "Dr come she's convulsing" da sauri yay ciki yana yana kallon Baba yace "just stay here" da gudu ya shiga dakin ya karbi handglove din da wata nurse ke mikamai yana sakawa a hannu yana kallon patient din sanan yace "ya za'ayi tana convulsing bazaku cire mata wanan hijabin ba, ku cire mata and someone should on the AC" yafada ba wasa sanan yakarasa inda take bayan yagama saka hand glove din, ahankali yakai hannunshi yajuyo da ita, tareda karban wani kalan spoon da nurse kebashi yakama kumatunta ya matste bakinta yabude yasa cokalin abakinta gudun karta taune harshenta, zafin dayaji ajikinta saida yabashi tsoro, sanan ya karbi alluran dayasa abashi yakama hannunta yanemo jijiyanta yamata allura, ko minti daya ba'a daukaba tadena convulsing yay stabilising nata, yasake saka wani sabon alluran ya debo jininta awani a syringe din yabama wata nurse yace to the lab" sanan ya kalli wata nurse yace "send in the father" fita tayi bata jimaba suka shigo tareda Baba hakan yasa sauran nurses din suka fita shikuma yadauki wani paper da byro ya kalli Baba dayaga yaje ya tsaya akan Fatima yana kallonta yace "ya sunan yarka Baba"? batare daya kalleshi har lokacin idanunshi nakan Fatima yace "sunanta Fatima Zarah Muhammad" gyadama Baba kai yayi bayan yarubuta yace "meya sameta, meka damunta, tamaka complain wani abu namata ciwone"? Ajiyan zuciya ya sauke yace "ni jiya narabu da ita Ipy kafin natafi aiki, nadawo gida wajajen goma sunyi bacci, saida safen nan kaninta yakirani nazo naganta babu lafiya, ciwon cikine na al'ada dakuma ciwon kai" rubutawa yayi sanan yace "daman haka yake mata"? Gyadamai kai Baba yayi yace

"eh haka yake mata amman kusan watananni biyu dasuka wuce ko ciwon kai batayiba sai wanan watan kuma, sumanta kusan uku agida, kome taci sai amai, batada karfi ko kadan, tun dare babu aiki sai kuka" sake rubuce rubuce yayi sanan ya ijiye takardan yadauko wata paper yay rubuce rubuce sanan yamikama Baba yace "yanzu dai kafara zuwa kasayo wayan nan magungunan a pharmacy kafin result din test dinta yafito mufara treatment yanzu kawai stabilising condition dinta nayi ba'a mata komiba tukunna sai kaje kabiya kudin kati da folder abaka ka kawomin anan da magungunan."

_G&G NATURALS wato Glow and Go Skin kenan, wanan kampanin ni nakan kirasu mane da transformation dan suna saida wani Body and face scrub da idan kakai amfani* dashi ko jariri bazai nuna miki taushin jikiba, sanan yana cire dead skin, acne dakuma pimples, black spot da sauransu kiji fatarki washar gata tai wani ubaaan laushi, suna saida wani gangariyan black soap, dakuma glow oil, kikai amfani da products dinan nasu kowa ya ganki saiya yaba, me kike jira Anty na? Kira daya kacal ya isheki kisami kayansu, suna tura kaya kowani gari, zaki iya tuntubarsu ta wanan number wayar 08144513333, zaki iya following nasu a Instagram @G&GNaturals

💫 _DISASTROUS LOVE_💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

✍M SHAKUR

EPISODE5️⃣
_FREE PAGE_

Karban takardan Baba yayi kaman mara lafiya yajuya yana tafiya ahankali yafita daga dakin yay

reception, tsayawa awajen yan kati yayi yabude  kati da folder, folder dubu daya, karamin kati kuma  dari uku yarage duka kudin saura dari bakwai, bai karayaba yarike komi a hannunshi yawuce Pharmacy ya tsaya gaban kanta tareda mika musu takardan da Dr yabashi, gani yayi anciro gorunan ruwa, allurai daban daban dawasu magunguna ankawo gaban table anyi wani tabe tabe a computer sanan aka fitomai da wata yar takarda, namijin wajen ya mikamai yace "Baba ga takardan biyan kudi je chan wajen account kabiya kudin saika dawo mana da takardan biyan kudin saika amshi magungunan katafi" karban takardan yayi ya kalli kudin dake rubuce awajen dubu takwas da naira Dari da talatin wani irin mugun faduwa gabanshi yayi ahankali yajuyo ya kalli saurayin dahar ya juya yakoma wajen zamanshi, dan gyara muryanshi dayaji ta shakemai yayi yace "Yallabai jimana" tasowa saurayin yayi yazo yace "gani Baba" cikeda damuwa Baba yace "kaga y'ata ce ba lpy, rai a hannun Allah, duka duka yanzu chanjin hannuna basufi dari shida ba, nace kozaka bani abubuwan nafara kaima likita afara mata treatment, inyaso kafin mubar nan wajen saina biya kudin daga baya yanzu dai afara bata taimakon gaggawa" dan murmushi pharmacist din yayi yace "Baba kenan, kayakuri Baba bama haka awanan asibitin" yanamai maganan yashiga attending to wasu mutane dasukazo wajen siyan magani, gajiya da tsayuwa Baba yayi awajen kafin ahankali yadaga kafafuwan shi dayaji sunmai nauyi sosai yawuce yafita, ahankali yake tafiya haryakai wajen parking space, sabida kar mutane su ganshi yasa ya zaga ta gaban motoci yazauna kan dakalin wajen yay shiru yana kallon folder da katin daya bude mata ga sunanta ajiki baro baro, Fatima Zara'u Muhammad, yarinyar nan tun tana yarinya wahala take yanzu gashi tana ciwo baida kudin kulada ita, jiya da yafita neman kudi yaje babu wanda yasani dayabashi kudi koda sisine, Rukayya ko yasan ko Mutuwa Zara'u zatayi bazata taba cire kudin ta tabada ba, dudda yasan itama ba lallai yasamu irin wanan huge kudin a hannunta ba amman bazai rasa yarsu dubu dubu biyuba, toya fita yay bara ne? Ya tambayi kanshi, but ayanda duniya ta chanza babu wanda zai ganshi yanzu haka ya yarda yabashi kudi yayi tsaf tsaf dashi gayar shaddar shine tsaf tsaf ne za'a yarda abashi taimako, jiyayi wasu hawaye masu shegen zafi sun zubomai yakai hannu ya share amman suka kasa dena zuba hakan yasa kawai ya barsu suka slcigaba d kwarara.

Agogon hannunshi kirar iwatch dake daure a wrist dinshi ya kalla about 25min kenan Baban Patient dinan bai dawoba, dagakai yayi ya kalli yarinyar ganin har yanzu she is stable bacci take yasa yadauki stethoscope dinshi yarataya awuya ya kalli nurse din dake wajen yace "stay with her, idan her Dad yakawo magungunan call me, idan ta tashi call me" yana maganan yajuya yafita daga dakin yay hanyar fita waje batare daya kalli dumbannin mutanen dake GOPD ba, tun 4 nasafe ya shigo asibitin nan emergency baici komiba har yanzu yunwa yakeji sosai by 1 yakeso yatafi gida yahuta yay bacci, wajen parking space yakarasa yay wajen wata hadaddiyar Black suv bude motar yayi da key dinshi sanan yamika hannu yadauko wani haddedden moderate flask dake kan dayan sit din gaban mota, bude marfin flask din yayi da saurinshi sabida tsabaragen yunwan dayakeji yakai flask din bakinshi yana kwalkwalan coffee dake cikin flask din daya hada da asuba dazai fito, saida yay kusan rabin flask din sanan ya sauke daga bakinshi yana sauke ajiyan zuciyan gajiya, saida yadan huta sanan yadaga flask din zai kara komar dashi baki kaman ance ya kalli bangaren damashina ke parking ya hango wani mutumi dan magidanci dabai ganin fuskarshi da kyau zaune gaban wata mota a side dinshi rikeda

folder a hannunshi yana share hawayen dake bin fuskarshi looking so confused and sad, jiyayi zuciyarshi ta tsinke dan haka Allah yayishi yanada tausayi sosai, kasa cigaba dashan coffee shi yayi dudda uban yunwan dayakeji, maida flask din yayi ya ijiye, yamaida kofan yarufe yamata key sanan yataka ahankali yana tafiya harya isa inda Baba yake zaune kanshi akasa yana share hawayen dake zubomai baima lurada wani yazoba dan hankalinshi yay nisa yana tunai. "is everthing okay Sir, mesa kazo nan kazauna kana kuka"? Wata zazzakan muryan da Baba yaji akanshi namai magana cikeda kamala hakan yasa yadago kanshi da sauri da idanunshi dasukai jajir yahada ido da Dr daya rubutamai maganin Zara, Dr na ganin Baba yaganeshi shima at a spot ai mutumin dazune Baban yarinyar dake emergency ward, ganin Baba yace "what is it Sir? Mesa kazonan kake kuka ina magungunan danace kasayo"? Dr yay tambayan yana kallon Baba yana kara nazarin yanayinshi, baki Baba yabude zaiyi magana saikuma wani irin takunkumin bakin ciki yakara tokaremai wuya wasu hawayen suka sake zubomai, kaman wanda notin kanshi ya kwance baisan lokacin daya kwaso yan chanjikan dasuka ragemai ba a aljihu yanuna ma Dr idanunshi sunyi jajir ga hawaye sun cika idanun kana ganinshi kasan he is pain yace "kagansu wanan ne kudin danake dashi gaba da baya, banda hanyan samun wasu, Zara'u na nachan kwance rai a hannun Allah an rubutamin maganinta nakasa saya sabida bandashi, bandashi, ina zansa raina? Asibitin gwamnati ma nakasa biya ba dole nazo nan na zauna ba likita" yanda yake maganan kaman ma wanda baya cikin hayyacinshi tsabagen damuwa yasa Dr yacigaba da tsayuwa a inda yake batare dayay motsi ba yay shiru yana kallonshi kawai, hawaye Baba yasake sharewa yace "Kaga Zara'u itace y'ata ta farko, tunda yarinyar nan tazo duniya bata tabajin dadi naba ni Mahaifinta, bana saya mata kaya, kaya irin nakowace yarinya budurwa datake tasowa, Zara'u bata tabamin korafi ba kokuma tace saina mata, yarinyar nan bata taba bude baki ta tambayeni abuba, kotamin korafi kotanunamin bacin rai, banmata kayan salla, bansiya mata takalmi, babu abinda nakema Zara'u sabida bandashi, yarinyar nan bata taba yimin kocemin Baba yimin kaza ba, yarinyar dake tausayin mahaifinta nake wahalarwa haka gashi yanzu ma datake rashin lpy nakasa mata komi, wlh ban cancanci zama mahaifint........" kafin Yakarasa maganan Dr ya tsugunna da sauri yakai hannunshi kan bakinshi hakan yasa Baba yay shiru yana kallon kyakkyawan fuskar Dr dake sanye da glasses, cikeda tausayi Dr yajanye hannunshi daga bakin Baba ganin yadan natsu yana kallonshi, hakanan yaji Baba ya mugun bashi tausayi, ahankali yace "Sir ba'a magana haka, Allah daya baka yarka yasan ka chanchanci zama mahaifinta ne saisa yabaka ita a matsayin y'a, sanan aganina godiya yakamata kama Allah daya baka y'a irin wanan wanda tun anan duniya take jinķanka, and just because bamu bama yaranmu abinda yakamata mubasu ba, or bamu wadatasu da kayan alatun duniya ba ba doesn't mean we are not good fathers to them, karka kara magana haka Sir, I know yarka na alfahari dakai, and stop crying, yanzu dai nawane kudin magungunan"? Ahankali Baba yace "8150 sukace" gyadamai kai Dr yayi sanan yamike tsaye yakai hannunshi bayan wandonshi wallet dinshi yaciro yabude yazaro wasu kudade yan dubu dubu dashi kanshi baisan yawansu ba ya tsugunna, hannun Baba yakama yasaka kudaden aciki yace "jeka sayo magungunan kazo mufarama yarka treatment ko" yay maganan yana sakinma Baba coolest smile dake comforting any kind of heart, wani natsuwa Baba yaji ya shigeshi tareda sake rike kudin da kyau yana kallon fuskan Dr ya nisa zai bude baki yay magana wayan Dr dake aljihun lab coat dinshi yahau ringing ciro wayan yayi yana mikewa tsaye yana gani inda ake kiranshi yatashi da sauri yajuyo ya kalli Baba yace "get magungunan

now ka kawomin she's convulsing again" da gudu yajuya yabar wajen shima Baba sake damke kudin yay gam gam ya tattare su folder yatashi yay pharmacy harda gudun shi.

Da sauri yatura kofan yashiga dakin nurses kusan uku ke kanta suna kokarin tura mata wani abu abakinta sabida yanda ta taune hashenta kadan har yana jini daya daga cikinsu tace "wai where is her father da magungunan"? Karasawa inda suke Dr yayi yana kallon yanda bakinta ke jini yace "me aikinku? Ya akayi kuka bari tajima tongue dinta ciwo"? Yay maganan yana grabbing kumatunta da kyau ya karbi abin yasa abakinta sanan ya karbi alluran dasuke bashi yakara pushing a jijiyanta cikin sakan daya tadena convulsing, hakan yasa yace "are the test result not ready"? Bashi wata takarda sukayi hakan yasa ya karba ganin result dintane zai duba daidai lokacin Baba yashigo dakin da mugun saurinshi yana kallon Zara ganin jini abakinta yasa yabude baki zaiyi magana da sauri Dr ya karbi magungunan da folder daga hannunshi yana mikama nurses yace "Baba she is fine yanzu zamu fara treatment kaje waje kajiramu kaji" fita Baba yayi adimauce yarufe kofan dakin dawowa ciki Dr yayi yahada kayan yazo yamata fixing drip sanan yahada wani allura wanda shi a duwaiwai zai mata sanan yarufe yazo ya tsaya akanta, fuskanta yadan kalla wanda zai iya cewa kusan sai yanzu ne yakalleta da kyau yarinyar ko ta mugun kama da mahaifinta itama farace kall kaman shi, ahankali ya ijiye alluran sanan yakai hannayenshi yadaura kan hannunta yadan juyo da ita ahankali ta side, riganta yadan daga sama kadan idanunshi ne suka sauka akan farar fatar jikinta kaman na jaririya ga dan gashi kadan kadan sun kwanta sunyi lub, hannunshi yasake kaiwa yadan ja zaninta hade da pant dinta kadan sanan yashafa spirit kafin ahankali ya chaka mata alluran motsin dayaji tayi yasa yadan waigo ya kalli fuskarta gani yayi ta yatsine fuska cikin bacci, cire alluran yayi yamika ma nurse din ta karba tasa a bola, sanan yajuya yace "ku tsaya da ita I will be back in the next 15min" yafice daga dakin Baba na ganinshi yatashi yace "Dr yatake"? batare daya kalleshi ba yace "muje office dina" binshi Baba yayi har zuwa office dinshi zama yayi tareda nunama Baba kujera Baba ma yazauna yace "meke damunta Dr naga jini abakinta" dan murmushi yayi yace "wanan ba matsala bane taune hashenta tayi kadan, I called u ne danna fadamaka I don't think zamu sallami yarka yau, result yafito tana dauke da maleria da typhoid masu karfi wanda sune ma kesata wanan convulsion din, gakuma ciwon mara at least zamu iya riketa na kwana daya ko biyu haka" shiru Baba yayi yana kallonshi cikeda damuwa, murmushi Dr yayi yace "karka damu zanyi settling hospital bill din wanan kudin hannunka ka rike na abinci dawasu abu ko" shiru Baba yayi saikuma chan ya nisa yace "Ya sunanka likita" anatse yace "sunana Imam Naseer Marafa" girgixa kai Babba yayi cikeda gamsuwa, yace "kaidan aljanna ne Naseer, Allah yamaka albarka, Allah ya saka da alheri da taimako na dakayi, azamanin nan da wuya ake samin likitoci irinku, awanan zamin likita iyaka kabiya yay treating naka, idan baka biyaba babu ruwan shi, Allah yamaka abinda kakeso kaji Naseer" shiru yayi yana kallon Baba kafin ahankali yace "Ameen nagode sir" Tashi ahankali Baba yayi yace "bari nabaka wuri" gyadamai kai kawai yayi Baba yawuce yafita, bin bayan Baba yayi da kallo yay shiru kaman wanda ke tunani kafin ya fuzarda iska ahankali ya jingina da kujeranshi tareda lumshe ido dan yagaji sosai.

Bude kofanshi da akayi aka shigo yasa yabude ido kadan ya kalli kofar, wata female Doctor ce

mace kyakkyawan gaske doguwa tana sanye da atampa golden da dige digen pink ajiki, ta yana kanta dawani pink gyale chiffon plain bakomi ajiki saikuma lab coat dinta fari kal yasha guga sai kamshi take bazawa wajen aljihun ta an rubuta Dr Zee ajiki, maida idanunshi yayi ya lumshe ganin itace, karasowa ciki tayi taja kujera tazauna tace "Dr Helper koma Dr Charity zankiraka am here i need help too pleaseDr" dan yatsine fuska yayi alamun he's not into her silly talk, murmushi tayi tace "okay joke apart Dr Imam, I just came in, namanta da stethoscope dina agida kuma idan HOD yaganni wlh zansha fada, please kindly aramin naka kaji kasan Helper is your second name right Dr nice" tai maganan tana kallonshi tana murmushi cikada tsokana, ahankali yabude idanunshi kadan yadan kalleta saikuma ya yatsine fuska yace "wai why are all this intern Doctors not serious haan"? Dan murmushi tayi, hakan yasa yadaure fuska yace "ina magana kina murmushi, alright go and find stethoscope awani wajen not here" da sauri cikin kara narkan da murya kaman zatai kuka tace "no fa, ni wlh badakai nake ba" ganin yaki kulata saima wayanshi daya ciro yana kunnawa yasa tace "kasandai idan HOD yakamani bani kadai zaiyi scolding bako dan ai yasani akasan kane" dagokai yayi ya kalleta baison surutu idan kuma akwai macen dayataba gani aduniyan nan datafi kowa surutu is this girl, baimasan mesa HOD su yasata under him ba, dan gajeren tsaki yaja strictly yace "tashi kidau stethoscope daga that drawer and get out of my office Zeenat" yay maganan yana mata pointing drawer dake facing su a other side of the office wall, tashi tayi ahankali tai wajen drawer tana kara nanata yanda yakira full name dinta yau, ahankali ta sanya hannayenta taja drawer tabude taciro wani sabon stethoscope mai kyau blue tadauka sanan tamaida drawer ta juyo ta kallai gani datayi yasake lumshe ido kaman mai bacci yasa murya chan kasa tace "thank you Dr Imam" sanan tadaga kafa tai hanyar kofa harta murda kofan zata fita sanan yace "Dr Zeenat" da sauri tajuyo tadan bude manyan idanunta da mamakinta jin yakirata, folder yamika mata yace "this my patient tana Emergency, monitor her, I've written everything anan idan time yayi push d injections ma left hand veins dinta, i repeat left hand, idan any complications arise give me a call, idan kuma condition dinta yay stabilising move her to ward, zanje gida yanzu under no condition should u leave his hospital saikinga dawowana" kaman zatai kuka da sauri tace "waimena maka daga zuwana zaka hadani da irin aikin nan, yanzu harsaika dawo zan tafi? Inada bridal shower dazanyi attending fa by 5pm" tai maganan tana batarai sosai, dauke kai yayi yashiga tattare kayanshi tana tsaye tana kunkuni, lab coat yacire yarage dagashi sai kananun kayan dake jikinshi yadau wayanshi da car key dawani folder yazo zai wuce ya watsa mata wani mugun kallo, hadiye maganan tayi tareda sunnar da kanta kasa dan jitayi yacika mata ido bazata iya kallonshi ko cigaba da korafin ba yawuce yafita yabarta tsaye anan, takai kusan 2min dukan kirjinta bai dawo daidai ba sanan tasamu tabude kofan tafita har lokacin kamshin shi takeji.*

💫 _DISASTROUS LOVE_💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

✍️M SHAKUR

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

EPISODE 6️⃣

_FREE PAGE_
Fita yayi direct zuwa parking lot, motarshi yabude ya shiga yatadata yawuce yafita daga asibitin, agaban wani Baban gida a GRA yay horn ko sakan biyu ba'a dauka ba aka bude gate din yasa kan motar ya shiga ciki, packing yayi zai fito mai gadi daya rufe gate din yataho dagudu yace "angaida likita, Baban ka likita, Mamarka likita sannu ka da zuwa dan Alajin naira Alaji mai mutane nakowa" cikeda gajiya yasakamai key motarshi a hannu kaman zaiyi kuka yace "Ohhh i am not in for this your kirari Musa yau, ga key nan grab my things ka kawomin side dina and lock my car" yay maganan tareda juyawa yawuce abinshi, tsayawa Mai gadin yayi yarike kugu yakai yatsarshi daya kan kanshi yana tunani saikuma chan yanisa yace "wai ni da likita yaketamin yaren nan yadauka nima likitan ne yau, memawai yake nufi" "cha yayi ka kwashe kayan daya bari amota ka kaimai flat dinshi sanan karufemai mota" da sauri yajuya jin zazzakar murya na magana wata doguwar yarinya ce dabazata wuce 19 , 20ba, tana sanye da doguwan rigan atampa kanta a tsafe bama'a tajeba daga gani tsifa ake mata, harara mai gadin yaballa mata itama ballamai tayi tace "kazami kawai" da sauri yace "wlh saina hadaki da likita" gwalo tamai tajuya takoma flat dinsu shikuma ya shiga kwashe abinda akace ya kwashe sanan

yawuce yay wani flat da shikadai ne daban agidan, sallama yayi tareda bude kofa yashiga ciki, falone hadadden gaske kal kal sai kamshi yake komi na dakin off whitene, shiga ciki yayi yana kalle kalle yace "dadina da likita akwai tsafta, kaga daki kaman nakara mai da yaji akai na ci tsabagen ban sha'awa" ijiye komi yayi kan centre table din sanna yawuce yafita yana kara waigen falon.

Sosai yabata lokaci sanan yafito yana sanye dawani short H&H 3quater milk color, yasanya wata black plain t-shirt, wanan karan babu glasses akan idanunshi hakan saiya kara bayyanar da kyawun kwayan idanunshi dasuke nan farare kal kwayan idon kuma bakake kirin, silipas yasaka sanan yabude kofa yafice, Baban flat din gidan ya shiga, wasu yan matane su uku ne a falon suna zaune suna kallo, suna ganinshi kowacce ta natsu atare suka gaidashi "Ya Imam good afternoon welcome" gyadamusu kai kawai yayi yace "how come banga ku fara shirin islamiyya ba" karaman cikinsu mai 19yrs din wacce ake kira da Rayyana ce tace "Ya today is Thursday fa" gyadakai yayi yace "oh okay, where's Ammi"? Kafinma subashi amsa sukaji murya datadan manyanta ance "anya akwai randa Imam zai iya dawowa gidan nan bai tambayi maman shi ba, ai kaga abinda yasa nafiji dakai kansu wa'è" tanuna babban cikin yara matan mai suna Rahma tace "su yaran Babansu ne" dariya yayi daidai ta sauko ya rungumeta hannunta takai kan cikinshi tace "zokaci abinci oya oya, cikin nan babu abinci cikinshi" dining takaishi tazubamai abinci a plate sosai yaci abincin yay nak sanan yafara mata hira, aduniyan nan Ammi kadai yake hirada ita kaganshi awani waje zaka dauka bai magana ko dariya. Yatsine fuska yayi yace "Amma wlh nagaji da aiki at this government hospital, narasa maisa Dad baiso nai aiki a hospital dinshi" murmushi Ammi tayi tace "ai duk Dr dabai aiki a federal government hospital ba baida experience,  watarana zakaga abinda yasa Babanka choose that 4 you son, banda haka is just the matter of time ko" yatsine fuska yayi yatashi yamika hannu yadau cup din fresh juice yace "Ammi bari naje nadan kwanta, by 5 kitadani pls, 6 zan koma clinic" binshi tayi da kallo yawuce falo, kannin nashi ya kalla yanda suka natsu suke kallon zeeworld yace " kunyi salla"? Kasa amsashi sukayi saidai kowannensu yashiga tashi ahankali gudun karya makesu sukai stairs da gudu, girgixa kai kawai yayi yawuce yafita daga flat din zuwa nashi.
****

Ahankali take bude idanunta dasuka mata nauyi sosai tanadan yatsine fuska ganin haka yasa da sauri Baba dake zaune kan kujera gabanta yakai hannunshi kan kumatunta dakeda wani irin laushi kaman na jariri ya shafa taredakai fuskarshi yana leken idanunta datake kokarin budewa yace "Zara'una, Fatima Zara bude idanunki nine Babankine, ganinan taredake" ahankali take bude idanunta jin muryan Baba sama sama saikuma tabude idanun tass tadaurasu akan fuskan mahaifinta tanajin wani irin ciwon kai amman bakaman nadazu ba (safe). Jin hayaniya sama sama yasa taware idanunta duka da kyau ta kalli inda dake, karfe tagani da ledan ruwa kafin tabi igiyan da kallo taga yana hannunta sanan ta waiga tana kalle kalle ganin suna wani babban daki dake dauke da gadajen marasa lafiya guda goma side dinta biyar opposit dinta ma biyar,

yanda take kalle kalle yasa Baba yace "kina asibiti ne an kwantar dake" juyowa tayi ta kalli Baba kafin tayi magana Dr Zee data gama duba patient din kusada gadon Fatima ne takaro fuskarta cikeda annuri tana kallon Fatima data bude ido tace "ahhh yar gatan Baban ta kin tashi"? Dayake Zee akwai surutu ta kalli Baba tace "Baba Zara'unka ta farka ka barni nahuta yanzu, kasa naduba maka ita ko baccin lafiya take dazu yafi sau dari" sanan ta kalli Fatima tace "Zara bara infada miki wani abu Babanki nasonki sosai sosai da ace haka iyayen kowa ke sonsu haka da yara basu wahala aduniyan nan ba daduk munji dadi" dan murmushi tayi dudda ciwon kan dake cinta murmushi yasa dimples dinta suka lotsa sosai dasauri tace "auuuuu Baba yarinyar ka nada mugun kyau jibi wani cute dimples dasuka bayyana akumatunta dudda batada lafiya, Baba kuyan wani garine dan Allah"? Tai maganan tareda juyawa taja kujeran next bed dake gaban na Zara takawo gaban gadonsu kusada Baba zata zauna dantaji labari taji andaka mata tsawa. "What do you think you are doing Dr Zee"? Ba Zee kadai ba har Baba, Fatima dama duka yan ward din saida suka dagokai duk suka waigo, Dr Imam ne, yana sanye da black cover, black trouser, sky blue short sleeve t-shirt daya bayyana muscles dinshi manya manya, idanun nan nashi sanye da fararen glasses, gashin sajenshi sunyi lub lub sai uban kamshi yake zubawa hannunshi rikeda lab coat bairiga yasakaba yana kallonta babu wasa ko daya akan idanunshi, tsit kakejin dakin kaman ba'ai hallitta awajen ba, ahankali tahadiye miyan dataji yabushi abakinta dakyar ta iya dauke idanunta akanshi ta kalli agogo 6 na yamma daidai maisa batai tunanin lokacin dawowan shi yayiba taketa surutu, kasa magana tayi ta tsaya awajen chak, nan kakejin kus kus awajen masu jinya na daman ta ishemu sai shegen surutu ga Oganta nan ai yashigo, wasu na kus kus suna su basu taba ganin likita mai surutu hakaba wasu na ai kaman yar makaranta ce batariga tazama likitan bama, jin kus kus din dayan ward sukeyi yasa yahadiye fushinshi dan baiso ya disgata as it is yanzu ma was so embarrassing balle kuma yamata fada hakan yasa yace "go and wait 4 me in my office" da sauri ta gyadamai kai ta tako har zuwa inda yake abakin kofa tawuce tabi ta gefenshi tafice.

Yadan dauki kusan 1min sanan yakaraso ciki yawuce gadon Fatima inda yaga Zeena ta tsaya alamun anan take, yana karasawa kafinma yay magana Baba yabashi hannu yace "barka da zuwa likita" "ina yini Baba yamai jiki ta tashi"? Da sauri Baba ya kalleta ganin idanunta a lumshe yakira sunanta yace "Zara'u tashi bude idanunki Dr yazo dubaki" adan hankali Dr Imam yace "barshi tukunna sai Nurses sun mata wanka an chanza mata kaya taci abinci sanan zanzo naduba ta, Nurse" yakira biyu daga cikin nurses din ward din yamusu magana da yaren da Baba bayaji sanan yawuce yafita, tadata sukayi cuka cire karin ruwan, kasa tsayuwa tayi hakan yasa suka gunguro wheelchair.

Sosai take cije lips kaman zatai kuka sabida yanda takejin azababben ciwon mara har suka kaita bayin, daya daga cikinsu ne tadawo tace "ina kayanta Baba" da sauri yanuna musu yar karaman jakan daya sawo mata kaya, dauka tayi tawuce bayin da taimakonsu tana bala'in jin kunya suka mata wanka da ruwan dumi suka gyarata suka saka mata wani sabon pant da pad, wani aikin sai nurses all hail to our hospitals nurses, you people rock, Allah yabiyaku ladan aikin

dakukeyi Ameen!!!.

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

Wani doguwan bakin riga taga Baba yasayo nata babu gayu ajiki kana gani kasan mai araha ce amman tai kyau sosai, sai wani pink hula shima mai kyau daya kara haska fuskarta, sai kallon rigan take da idanunta dasuke juya mata, dawo da ita sukayi suka dagata suka sata akan gado shikuma Baba yabata shayin daya kadamata kasa karba tayi hakan yasa yace "sannu kinji" gyadamai kai tayi ahankali tanajin kuka, kaimata shayin yayi baki tadan kurbi kadan ko kadan bakinta bayamata dadi sai kallonsu suke yan ward din ana mamakin yanda Babanta ke dawainiya da ita, ba mamanta ba, wasu na halan batada mahaifiya ce daman gashi tai kama da Baban nata kaman yay kaki yatofar, gasu kyawawa kaman bayan Nigeria ba. Sosai tasha tea sanan tace ya isheta ijiyewa yayi sanan yace "indomie da kwai fa nasayo miki" dan yasan tanason indomie sosai, girgizamai kai tayi ahankali tace "zan kwanta Baba" da sauri yace "a'a bari kihuta kadan saiki kwanta likita ma zaizo yadubaki sanan za'a maidamiki da karin ruwan" gyadamai kai tayi kawai, ganin batajin dadi yasa yadau pilon gadon yasa ya jinginar da ita, dan murmushi tamai dan taji dadi shima murmushi yamata, ahankali tace "Baba yaushe kasayomin wanan rigan? Ina hijabi na"? Ahankali yace "dazu nasayo miki gashi tamiki kyau, kibar hijabin likita yasa aka ciremiki baga hula akanki nanba, kiji sauki tukunna" gyadamai kai tayi tana kokarin lumshe ido gabanta ya yanke yafadi da saida tadan zabura ta tashi daga jikin filon ta dafa kirjinta da sauri Baba yace "menene amai kikeji"? Yay maganan yana rike hannun data daura akirji zatai magana sukaji mutum akansu da sauri ta daga kanta da manyan shanyayyun idanunta dake cikeda zazzabi suka hada ido likitan daya dakama wanan macen likitan tsawane saidai yanzu yasa lab coat, kaman yanda take kallonshi haka shima yake kallon kwayar idanunta, Baba dake tsaye kusada itane yace "Likita barka da zuwa" batare daya janye idanunshi ba yace "barkada yamma Baba" yay magana yana tura hannu cikin aljihu yaciro wata yar touch light mai kama da byro yadan taka zuwa gaban gadon, jitayi kirjinta yacigaba da faduwa sosai da sauri ta janye idanunta ta saukesu akasa tareda sa hannu takama rigan jikinta tawajajen cinya ta rikegam, ahankali yajanye nashi idanun shima ya kalli Baba yace "Baba kadan bamu wuri zamu dubata" da sauri Baba yace "to" zaro manyan idanunta tayi dasauri kwalla yataru a idanun tabi Baba da kallo harya wuce yabar wajen nurse din dake tareda shine rikeda tray din injections tace "ba cinyeki zamuyi ba yanzun nan muna gamawa zai dawo kinji" gyadamata kai tayi ahankali idanunta na shining sabida kwallan daya cikashi, batare daya kalli nurse dinba yace "ja labule" jan labulen daya zagaye gadonta tayi na both side dana gaban gadon hakan yasa babu wani na cikin ward dazai iya ganinsu, ahankali yakai hannunshi zai

kama habarta da sauri taja kanta baya, dan dariya nurse din tayi tace "matsoraciya" wani kallo yama nurse din hakan yasa tai shiru tana hade hannayenta biyu alamun sorry sir, juyoda kanshi yayi yasake zubama Fatima shanyayyun idanunshi yakai hannunshi for the second time ahankali zai kama habarta komar da kanta baya tasakeyi shar hawayen kwayar idonta na dama ya zubo na haggun shima yacika fam yana shirin zubowa, da yatsa ta nuna nurse din tace "k....ki.....ra....min  Baba dan Allah" sai alokacin Nurse din tasake magana tace "toki tsaya Dr yadubaki bazai daukemu 2min ba sai Babanki yazo" bayan hannunta takai ta share hawayen sanan ta saukar da hannun tasake kama jikin riganta kanta akasa, ahankali for the third time yakai hannunshi yakama habarta yadago da kanta sukai eye to eye, hawayen kwayar idanun haggunta ne suka zubo sharrr sukabi kumatuntu sukai wuya.

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128*_

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_WANAN LITTAFIN IS 500 IDAN KINASO KIBIYA SAINA SAKI A GROUP, HAR YANZU INA FREE PAGE, 3107021073 AISHA MUHAMMAD FIRST BANK_
_FOR BUSINESS PROMOTION KO ADVERT CHAT ME UP ON WATSAPP 07012181461_

✍️M SHAKUR

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

EPISODE7️⃣
_FREE PAGE_

Toculan hannunshi ya kunna yana kallonta still, ahankali yabude bakinshi kaman wanda baiso yabude softly yace "stop crying" gyadamai fuskarta dake hannunshi tayi yana kallonta tahadiye kukan gabanta na faduwa sosai, haska duka idanunta biyu yayi sanan yasaki habarta yace "meke miki ciwo yanzu"? Kasa jure kallon dayake mata tayi tasake saukar da kanta kasa murya chan kasa tace "kaina" "damene kuma"? Dagokai tayi ta kallai saikuma tasake sauke kanta kasa takasa magana, karban folder hannun nurse din yayi sanan yace "raise her gown cover her legs with the bedsheet" sanan yajuya musu baya yana rubuce rubuce abinshi acikin folder ta. Fashewa tayi da kuka ganin yanda Nurse din ta kwaye mata riga ga namiji awurin, riganta har saman cikinta, saitaja bargon gadon tarufe mata cinyoyinta har zuwa kasan maranta, tundaga cikinta har maranta abude  sanan tajuyo tace "angama Dr" ahankali yajuyo yamika mata folder yana kallon cikin nata dayay lakur kaman batacin abinci sai maranta dayadan kumburo, handglove yasaka sanan yakai hannunshi yataba maran yakalli fuskanta motsi yaga tayi tareda runtse udamunta gam alamun tanajin zafi, ahankali yace "zafi"? Murya chan ciki dake rawa sosai danduk a birkice take jin namiji nataba mata ciki tace "eh" dagowa yayi yadauki kwalaben allurai 3 dake tray injection da nurse din takawo ya fasa ya zuko alluran a syringe guda biyu da karami da babba sanan yadaga alluran sama yana saitawa kaman ance tabude idanunta tabude alluran data gani yasa tawani irin tsandara ihu. "Babaaaaa! Baba wlh naji sauki kazo mutafi gida ni kar amin allura" da sauri yajuyo ya kalleta kwaye zanin da aka lullube ta dashi tayi tawani zabura zata sauka hannu daya yasa yariketa dan faduwa zatayi tana tashi yamikama nurse din alluran, kokarin kwace kanta tayi tafashe da kuka sosai tace "wlh wlh naji sauki ku kiramin Baba mutafi Allah kuwan, inkanama Allah karkamin alluran nan dan Allah Doctor, dan Allah dan Allah" ayanda take kuka take rokonshi he could feel her fear tundaga heart dinta and is not a good condition ama patient allura haka, da hannu daya yariketa yakai hannunshi daya kan bakinshi yana kallonta yace "shiiiiiiii inbakiso namiki alluran kiyi shiru bake kadai bane a ward dinan ba am I clear"? Gyadamai kai tayi tana wani irin nishi tana neme nemen alluran taga batagani ba, hakanan saiyaji tana tunamai Rayyana haka take itama batason allura, juyawa yayi ruwan goran daya gani kan kantarsu yadauka yamika mata yace "sha ruwa and calm down" yabude mata goran tareda bata karba tayi takai baki tana kalle kalle kurba tayi kadan tabashi da idanu yama nurse alamu taje ta bayanta, ahankali yace "ya isheki"? Gyadamai kai tayi yace "to kwanta" yanda yake mata maganan sosoft ysata natsu, kwanciya tayi ahankali yaja zani yarufa mata kafa batare daya kalleta ba, hannunshi yamika ya karbi allura daya yace " ki kalli bakina kome nafadi kifadamin test zanmiki okay inaso nagane daga wani lobe ciwon kanki ke zuwa" gyadamai kai tayi, ahankali yake mata wasu alamu da baki yakai alluran yamata daya gabaki daya batasani ba dan haka Allah yayishi baida zafin hannu ko

digi, yamata dayanma, murya chan kasa yace "mena fadi"? Ahankali tace "banjiba" murmushi nurse tayi tace "cewa yayi yagama miki alluran" tanuna mata empty syringe din, da sauri takalli syringe din saikuma ta kalleshi abinma mamaki yabata, danharara yasakin mata yace "katuwa mai tsoron allura" ahankali tasaki murmushi dan yanda yace katuwar was a bit funny, da sauri yadauke kai yakama hannunta yamaida mata da karin ruwan sanan yawuce yafita daga wajen aka yaye labulen nata ya shiga duba sauran patient din da Zeena bata dubaba tai shiru tana binshi da kallo tanajin ciwukan datakeji ajikinta na sauka kadan kadan tana mamakin inda Baba yaje saikuma tai tunani yatafi salla, juyowa Dr imam yayi yakalleta kaman ance ta kalli gadon dayake hada ido sukayi da saurinta ta dauke kai gabanta nafaduwa kawai saima ta lumshe ido.

Wuraren 10:30 nadare yagama komi zai tafi, fitowa yayi rikeda jakan laptop dinshi a hannu, hanyar ward dinsu Fatima yayi, awajen kofan ward din ya tsaya yana kallon ciki batare dasun lurada shiba danbai bude kofaba, yanabi bed by bed yana kallo haryakai gadon Fatima, zaune ya ganta Baba yasa filo abayanta yana rike da plate da indomie keciki da soyayyan kwai yana ganin plate din yagane namai shayin gaban hospital dinsu ne, indomie Baba yadeba da cokali zaikai bakinta, makemai kafada tayi tadan turo baki idanunta dake cikeda ciwo sukadan juya ahankali tace "ni Baba nakoshi" da sauri Baba yace "yakuri ci wanan shine na karshe, aini bansan akwai ciwon dazakiyi ki tsani indomie kiba, oya ci ci ci Zara'una" yakai cokalin bakinta yana mata murmushi, washe cute white teeth dinta tayi zata bude baki tai magana Baba yasamata indomie aciki dariya tahauyi tana taunawa shima Baba yahau dariya yace "yaushe aka haifeki yarinya bagashinan kinci ba" batarai tayi tana taunawa saikuma tahau dariya ahankali dan bata da karfi.

Ahankali yasaki dan murmushi yana kallonsu yana tunani who ever says money shine happiness karyane, happiness kauna ce, just look at this father and daughter gwanin ban sha'awa. Kaman ance Baba yajuyo yaga Dr Imam tsaye da hannu Dr Imam yamishi alamu dayazo batare da Fatima ta gansu ba, tashi yayi ya ijiye plate din yace "ina zuwa Zara'u" hanyar kofa Baba yayi hakan yasa ta kalli kofan hada ido sukayi da Dr Imam da sauri ta dauke kai, abakin kofa Baba yasameshi yabashi hannu suka fara tafiya sukai hanyar waje Dr yace "Baba daman i wanted to see you kafin natafi ne, akwai abinda nakeson na tambayeka" da sauri Baba yace "menene likita"? Dan jim yayi kaman wanda baison yin maganan saichan yace "Baba naga tabon duka, fresh shaidan bulala ajikin Zara'u, waye yamata wanan dukan Baba?"

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

Shiru Baba yayi yakasa cewa komi yama kasa cigaba da tafiya hakan yasa shima Dr ya tsaya kaman mai nazarin shi saichan ya nisa yace "Baba shirun dakamin ya tabbatar da kasan wanda yamata dukan kenan wanda nina tabbata bakai bane, ayanda naga kakeson yarka nasan bakaine zaka mata wanan dukan ba, Baba yarinyar nan bama wanan dukan bane na farkon dukan da aka mata ba dan jikinta da tabo dayawa, koma waye ke dukanta Baba hakkinka ne amatsayin ka na mahaifinta ka kareta, ka tsareta, mace ce tanada rauni sosai, abu kankani zai iyasa rayuwar ya mace yabaci dan haka dole ka kula, idanma rashin ji take bada duka zaku gyarata ba ai" ahankali Baba yace "bantaba ganin salahar yarinya mai biyayya irin Fatima ba, ko kadan batada rashin ji sai dumbin biyayya da girmama nagaba da ita" Shiru Dr Imam yayi yana kallon Baba ahankali yace "mahaifiyarta ke dukanta"? Girgizamai kai Baba yayi yace "batada mahaifiya" shiru Dr yayi saima yakasa magana, ganin haka yasa Baba yace "ni fulanin Maiduguri ne, mahaifiyarta buzuwar Maiduguri ce amman dukanmu dagani har mahaifiyarta rainon kauyene muba yan burni bane, a kauye mukai aure muka kuma tare cikin dangi da yan uwa da abokan arziki  harta haifamin diyata Fatiman nan dakake gani ayau, bazan manta ba, lokacin Fatima nayar shekara biyu da watanni zan fita kiwo da safe tahau kuka zata bini, haka takemin and muddin tabini tosaina siya mata plantain chips da ake saidawa a bakin gari nadawo da ita gida sanan zata barni nafita kiwo, haka na dauketa nace bari naje nasaimata wanan plantains chips dinan abakin express sabida tanason abin sosai, kauyenmu nakan express road ne na zuwa asalin cikin garin Maiduguri, kuma masu saidawa anan bakin titin kake ganinsu (hawkers) na dauketa namata makawuya da nufin innaje nasayo mata mukoma nafita kiwo, muna fita bakin titi nakira mai plantain zan siya mata, na karba daya nasa mata a hannu nasa hannu zan ciro kudi a aljihu nabashi bangama cirowa ba mukaji wani irin kara da girgizan kasa dabansan lokacin dana dauki Fatima data rusa ihuba na kankame ajikina, kafin kasani naga ana ihu ana gudu, ga hayaki wuta natashi daga cikin dajin dana fito...." yadanyi shiru tareda lumshe ido, yanda Baba yay shiru yasa yagane end of the story, ahankali cikin wata murya dazai nuna asalin damuwa yace "Allah ya jikansu" ajiyan zuciya Baba ya sauke yace "Ameen, hadadden bomb yan boko haram sukai amfani dashi suka tada kauyenmu tass wai warning sukama gwamnati, dagani sai Fatima muka rayu a kauyen mu gabaki daya dasu bomb din yatashi dan safiya ne basuriga sun fita ba, nida Fatima mun wahala aduniyar nan, neme neman aiki, kwadago, da leburanci shine yakawoni nan Kano, inda nasami wata baiwar Allah matar nada kirki sosai tabani machine ina express tana tayani rainon Fatima dan tanason Fatima sosai matar Fatima ke kirada Baaba, yaranta duk suna waje, da aikin danake nasamu nahadu da wata budurwa dake saida mana da abinci a tasharmu na yan achaba Rukkaya, naji ina sonta namata bayanin kaina tace taji tanaso na, nadauki Fatima na kaimata tanason Fatima sosai, Fatima na yar shekara biyar mukai aure, Hajiya tabamu yarmu tabarmin machine din cewa zasubar Kano, ranan Fatima tai kuka amman ta hakura, a kasan waje take zama bata cika dawowa Nigeria ba, amman duk intazo Fatima na zuwa wajenta" ahankali yace "step Mum din Fatima tamata dukan nan"? Gyadama Dr kai yayi ahankali saikuma yace "da farko dana aure Ruka tana bala'in son Fatima sosai, dayake bata haihu dawuri saida mukai kusan shekaru biyu Fatima na shekara bakwai ta haifi Habib to daganan kaman asiri son datake ma Fatima yakoma ki, kodan taga son danakema Fatima mai karfine oho, bawai bansan sauran yarana bane a'a kawai dai son Fatima dabanne araina, sabida tun tana yar yarinya take wahala bata taso gidan gatan uwa ba kona kakanni duksun rasu, ina matukar tausayama Fatima, yanda

kuma nake sonta haka Fatima take sona, ko ciwon kai yakamani yarinyar nan saikaga kaman zata haukace sabida damuwa, ina iyakan kokarina wajen kareta, ni kaina bansan da dukan ba sai dazu danaje gurin aikinsu d'ana Habib a samin iska a machine yake gayamin ai dukan da Mama ta mata yatada mata da ciwo" Ajiyan zuciya kawai Dr Imam yasauke sosai yaji Baba yabashi tausayi ainun, ahankali yamikama Baba hannu yace "Baba ka koma wurinta saida safe, gobe idan nazo taji sauki zan sallameku saita cigaba dashan magani, ka kulada ita" gyadamai kai Baba yayi Dr yawuce yatafi yabar Baba anan tsaye, Baba yadade tsaye awajen yana wani irin dogon tunani, da idan Ruka tama Fatima duka kowani abu yana tsawatar mata amman yanzu baya iyawa, dazu da Habib yafadi mai abinda yafaru ranshi yabaci ainun yatafi gida but yanazuwa daya kalli fuskarta kasa mata maganan yayi, ko kayan salla yace zai sayama Fatima tace mai bazaka siyamata ba zaiji rashin yabaci amman kuma saiya kasa mata magana, bazai kuma siyan ba, jiyayi kanshi na ciwo hakan yasa yahakura da tunanin yawuce yakoma ward.

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejarh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

Kwance yaganta kan gado tana kallon kofa kaman dama shitake jira ya shigo tana ganinshi tawani sauke ijiyan zuciya mai karfi, murmushi yamata yakarasa yaja kujera yazauna yana kallonta yace "jirana kike daman? Nadauka kinyi bacci Zara'una" dan karamin bakinra tabude tace "a'a" shiru yayi yana kallonta, kallonshi tayi itama sanan tace "Baba rigan nan dakasaimin nada kyau sosai ina sonshi" ahankali yadan duko da kanshi zuwa saitinn kanta anatse yace "maisa baki gayamin dana dawo da daddare Mamanki ta dakeki ba eh"? Yadanyi maganan ranshi abace, ahankali tace "Baba" cikeda dan bacin rai yace "duk randa tasake dukanki ko aka miki wani abu baki gayamin agidan nanba sai ranki yabaci Zara" ganin yanda ran Baba yabaci yasa taji hawaye sun cikamata ido murya chan kasa tace "kayakuri Baba" ganin yanda tai wani iri yasa yay murmushi yace "yawuce,  na gwada kiran lambar Baabar ki bata shiga bata kasar hala" gyadamai kai tayi ahankali, ganin har lokacin damuwa ne akan fuskanta yace "baki taba tambayana ya suffan mahaifiyarki yakeba Zara'una, ingaya miki"? Da sauri ta gyadama Baba kai,  murmushi Baba yayi yace "Mamarki doguwar mace ce sosai dan tafini tsawo saisa nai mamaki yanda baki wani dauko tsawonta ba, kuma shine abu na farko danakeso game da ita, inason doguwar mace saikuma yahadu da sunanta danake so shima Surayya, Mahaifiyarki nada yar doguwar fuska kaman taki anan, sanan fuskar nada dan fadi, tanada wasu irin idanu exactly irin idanun nan naki, zakiga acikin mutane idanunta dabanne, idan ta kalleki ne zaki kara ganin tsabaragen kyawun idanun, tanada dogon gashi baki kirin sanan yanada cika, kinga yanda kullum bakison tsifa sanan akama samu kikayin baki iya tajewa balle ki kulle haka gasjinta itama yake, tanada dan goshi dakuma jan lebe inda kika banbanta da ita kenan, ke kin dauko lebena pink itakuma nata jane kaman tasa jan jambaki, mahaifiyarki batada losewan

kumatun nan naki ni kika biyo da wanan, saikuma sanyin hali da hakuri dakuma juriya da kunya Fatima dukkin gado mahaifiyarki, saisa nake alfahari dake, dukmai hakuri da juriya yanacin riban rayuwa wata rana komin daren dadewa ki rubuta ki ijiye" ahankali tace "saisa bana fadamaka kome Mama tamin agida, Baba Mama tana matsayin uwace agareni, tabani kannai danake so sanan tarike ni cikinsu Baba bawai bazan iya fadamaka bane, kokuma bazan iya ina mata wasu abubuwan ko rashin kunya ko makamancin haka bane a'a, kariga ka koyardani hakuri dakuma juriya, banson tasanadiyata kana fada da Mama kullum, babu abinda nakeso aduniyan nan samada farin cikin ka, Baba kanada hawan jini banson abinda zai dagama hankali, kome nayi Baba nasan menakeyi wlh niba yarinya bane kawai kadinga mini addu'a kaji, nagama makaranta nafara aiki na kula dakai dasu Habib da dukanku" for the first time yau saiyaji Fatima tai magana kaman wata yar shekara talatin, hannunshi yakai kan kumatunta yana murmushi yace "Allah yacika miki burin ki, Allah yamiki albarka Zara'una, Allah yabaki miji nagari" murmushi tayi taja zani tarufe fuskarta tace "saida safe Baba kaina yafara ciwo mani" murmushi kawai yayi baisake cemata komiba idan sabone yasaba da kunyanta duk randa zai mat hiran aure ko magana suke karshen maganan yazo kenan dan guduwa zatayi.

_Deejerh Telecommunication offer data, TV cable subcription, and much more._
_Jama'a nakawo muku wata sabuwa wato Deejerh Telecommunications suna yima mutum data, suna tayaka biyan kudin subscription na Gotv, DSTV, startime harma da nepa bill zasu iya tayaki biya basaikin je nepa office kinbi layiba da sauran su, all abinda zakiyi shine kawai ki kirasu awanan number koki musu magana a watsapp 08107705128_

💫 _DISASTROUS LOVE_💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_FOR DIRECT MAGANA DA M SHAKUR A TUNTUBENI TAWANAN NUMBER NAN 07012181461_

✍️M SHAKUR

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design, graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number 07010439656 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._

EPISODE8️⃣
_FREE PAGE_
*******
Washe gari!!

Yau Jumma'atu Babban rana sosai ta tashi da karfinta kaman ba itabace tai ciwon dako tsayuwa bata iyayi jiyaba lallai Dr nan yasan kan treatment, dan dakanta yau tashiga bayi tai wanka ta gyara kanta tsaf dan bataso wasu kattin mata sumata wanka, kayan datasa jiya da za'a kawota ta maida bayan tacire doguwan rigan, tadau hijabinta ta saka daya mata wani irin mugun kyau, gawani haske datayi buuu sabida ciwon datayi idanunta sun fada sosai sunyi fari kallll kaman anzuba nusu farin hoda babu kwalli ko digi acikin su sai lips dinta dasukai pink yirrr suka tattare suka tsuke suka bushe sabida har yanzu da dan zazzabi acikinsu da ita kanta, sai wani pimple kwara daya rak data farka tajishi akan goshinta daidai in-between giranta guda biyu kuma yaydan kato kanagani kasan pimple din period ne, tana kallon pimple din a madubin bayin taji tana tura baki dan yasa tai wani iri ga idanunta sundan kumbura sunyi nama irin na mara lafiyan nan, muryan Baba dayazo gaban bayin ne taji yana mata magana. "Zara'u me kikeyi kika dade haka abayi Dr yazo dubaki har an wuce gadonmu" kalman Dr da Baba yafadi hakanan saitaji gabanta yafadi takasa magana. "Zara'u kinajina ko zazzabin yatashi ne" jin muryan Baba adan rude yasa tace "nagama gani nan" tai maganan tana bude kofa tareda daukan kayanta data saka a leda tafito binta yayda kallo dan saiyau yakara ganin hijabin da kyau yace "a ina kika samu hijabi haka daya miki kyau haka Zara'u"? Yamata tambayan yana karban ledan hannunta da kayan data cire ke ciki, murmushi tayi tace "Baba wlh Maryam tabani, na islamiyyan mune ta dinko mana" dan tabe baki Baba yayi yace "iyye yar gatan Maryam, ba laifi Hijabin yamiki kyau kwarai" turomai baki tayi adan shagwabe tace "Baba balaifi nema kyan dayamin din?" Dariya yayi yace "nidai kinga tafiyata idan kuma kika bari Dr yatafi bai dubaki ba baza'a sallameki yanzu da safen nanba sai likitan rana yazo" Baba yay gaba abinshi dayake

bayin abayan wani corridor dake cikin ward din yake, ganin harya fita daga lungun yay cikin ward dinsu yasa dadan saurinta tabiyoshi kanta akasa kafafunta na cikin wasu flat shoe baki irin yan dari biyar dinan.
Tana cikin tafiya dudda kanta na kasa ko kadan bata lurada bawon ayaba da yaron wata mata ya yar a tsakiyan ward dinba tana zuwa ta taka da kafarta, bawon ayaban yakama kasan takalmin ta daga kafan ta kai kasa zatai taking another step yawani yaja gaba zuttt tatafi tagaba gabaki daya zata fadi saikace anjawota da karfi ne kawai taji ta tafi ihu tayi sosai tana kokarin hana kanta faduwa tana watsa hannunta trying to stop kanta daga fadin. "Baaaaaaba......" shiru tayi batare data karasa kiran Baban ba jin ita bata fadi akasaba sanan ita batamasan a ina takeba takamaimai ammman dai bata jita akasa ba ta runtse idanunta gam tana nishi takara rike whatever hold her da kyau da fararen hannayenta ta rike gaban rigan ta daidai huge chest din da sauri da sauri kirjinta nawani irin mugun faduwa kaman zai rabe biyu, duka abubuwan nan sun farune aduka cikin sakanni dabasufi uku ba zuwa biyar, ahankali ta shiga bude idanuwanta dasuka shiga rawa kadan kadan kafin tabude su yan kadan, clean fararen kwayoyin idonta ne suka hadu dana Dr Imam dake sanye da fararen glasses yana cikin farin lap coat wanan karan ba stethoscope awuyanshi just him ne, gabaki daya tana cikin hannunshi yatarota, hannayenta duka biyun nakan kirjinshi tarike labcoat dinshi gam gam, yanda suka hada ido yasa ta maida idanunta ta kullesu da gudu gam gabanta nawani irin dukan uku uku daharshi kanshi yanaji ta kame kam tamakasa wani abu, duk cikin yan sakanni dabasufi goma bane akai abinanba daidai lokacin Baba ya iso wajen da saurin shi yan ward ma sukahau ihu.
"Subhannallahi assha, waya yarda bawon ayaba akasa, zasu kara nakasa yarinyar dabata dade da farfadowa daga ciwo ba" Baba daya karaso wajen da sauri yace "Zara" kaman wacce aka mintsila tasaki riganshi da sauri ta tashi tareda kabarda hannunshi dake waist dinta kaman tana kabarda kyankyaso tafita daga jikinshi da gudu jikinta narawa sosai zatai wajen Baba dake kusada Dr ayaban dake kasan takalminta har lokacin yakara kwasheta tai kan Dr, harwani wuntsila hannu take sabida yanda take tsoron fadawa kanshi amman saida tafada kirjinshi dan at this time ta gwammace tafadi akasa shima dudda yanada daman a kauce tafadi akasan but bai kauceba fadowa tayi cikin kirjinshi fuskarta yay slapping chest nashi, chest dinta da nashi suka wani hadu suka buga juna yasake riketa ta hanyar kai hannunshi bayanta, da sauri Baba ya tsuguna kafinma tafito daga jikin Dr ya kama kafarta yacire takalmin sanan yadaye bawon ayaban yay wajen bin dake cikin ward din ya wurga sanan yadawo daidai itama tafito daga jikinshi ahankali ko'ina najikinta na bari kanta akasa yan ward namata sannu amman ko kadan she's not comfortable, hannunta Baba yakama yace "sannu kinji ciwone" girgizamai kai tayi jikinta narawa har lokacin bata dawo daidai ba, janta Baba yayi yace "Allah ma yakiyaye dabadan likita ba Allah kadai yasan irin faduwan dazakiyi muje ki zauna" yay hanyar gadonta da ita yan ward sai sannu suke mata dan babu wani wanda ya lura da abinda yafaru tsakaninta da Dr all abinda suka gani is Dr saved wanan kyakkyawar patient din daga fadi.

Har suka koma suka zauna a gado Dr Imam yakasa motsi daga inda yake, Zeena dake tsaye gaban gadon patient din dasuke dubawa daya barta yatare Fatima ne da bawon ayaba ya zamar da ita batare data kalleshi ba tace "komu dawo later mu karasa ward round dinne"? Dan juyowa yayi, saikuma ya sauke ijiyan zuciya yatako yazo wajen ya tsaya gefen zee din yana

duba patient din yace "kin duba vitals dinta"? "Uhm" ta amsashi atakaice tacigaba da rubutun datake a folder sanan tamikamai karba yayi yaduba sanan yama matar alluran dazai mata sukabar gadon.

Tunda Baba ya zaunar da ita kan  gadon take ba daidaiba kanta na kasa tana wasa da yatsunta dake nan dogaye ga kumbunanta farare fat dogaye masu bala'in kyau da kauri, kar kar dasu. Muryan Baba taji yana "barka da zuwa likita" karban folder ta yayi daga hannun Zeena yana dubawa batare daya kalleta ba yace "any complain? Kinji sauki" gyadamai kai tayi ahankali  da sauri Baba yace "yi magana mana Zara'una" adan hankali cikin siriryar muryanta tace "da sauki" matsar da folder yayi daga saitin fuskanta ya kalleta, kanta na kasa har lokacin tana wasa da yatsunta sai bantalar kunbunanta take da basu fito bama, pink lips dinta kadai yake iya gani, saikuma goshinta da gashi suka kwanta sukai lub lub ga zufa datakeyi a goshi sosai dudda ward din babu zafi dan akwai AC gakuma fankoki, duk kallonan yamata cikin yan sakanni ne sanan yarufe folder yamikama Zeena dake gefenshi yakarasa ya tsaya agabanta danhar kafafunta na gogan nashi, wani irin yawu tahadiye takasa dagokai har lokacin, hannunshi yasa a aljihu yaciro yar toculan shi ahankali yakirata kaman baison yakira. "Fatima" dagokanta tayi adan hankali hada ido sukayi idanunta sun cikada kwalla sosai, ahankali yakai hannunshi kan habarta ya kunna toculan ya haska idanunta yana kallonta murya chan kasan makoshi yace "crying angel" ayanda yay maganan daga ita sai shi zasu iyaji, juyowa yayi ya kalli Baba  yace "zan sallameku Baba, zan baku maguguna dayawa, wanda every month dazaran ciwon maran zai fara zatasha, but nan da 7days zaka dawo da ita naduba ta" yay maganan yana bama Baba wata yar takarda yace "kabasu wanan zasu baka magungunan Allah kiyaye hanya" yay maganan batare daya jira maganan Baba ba yajuya yafice da sauri Baba yabishi har waje yanamai godiya dakuma addu'a daban daban.

Already Baba yariga yahada kayansu daman bawani abu garetaba banda kayan sawanta kala daya, daman abinci awajen mai shayi yake siyan mata, ledan kayan nata yadauka sanan suka shiga yima yan ward din sallama sukuma sunama Fatima Allah yakara sauki yasa kaffara ne fitowa sukayi yana gaba tana biyeda shi sukai hanyar pharmacy, ganin da dogon layi awajen yasa yajuyo yabata ledan kayan yace "rike ledan jeki sami kujera ki zauna chan na karbi maganin saimu tafi ko" gyadamai kai tayi tawuce ta tafi kujerun dake nan GOPD tasami wuri ta sauna a kujeran dake layin gaba inda mata uku ke zaune akan kujeran masu ciki sai ita data sami gefensu ta zauna tai shiru kawai kanta akasa danhar lokacin bata dawo daidaiba burinta kawai subar asibitin su koma gida, matan sai kallonta suke. Gabanta dataji ya yanke yafadi yasa tadan saki wani irin ajiyan zuciya kaman ance ta daga kanta suka hada ido da Dr Imam daya fito daga office dinshi wanan karan babu labcoat ajikinshi yana sanye da wata hadaddiyar bakar yadi mai digon fari fari, wanan karan ba cover ce akafarshi ba flat black Louis Vuitton takalmi ne akafan daya kara haska farin kafarshi, yay wani irin kyau bakin yadin yakara fito da

hasken fatarshi, yanda kirjinta ke bugawa yasa ta janye idanunta da sauri ta saukar da kanta kasa ahankali ta shiga wasa da yatsunta tanajan hijabinta tarike gam, tadau kusan minti uku ahaka sanan ta sake dago kanta ta kalli direction din data ganshi hada ido suka karayi har lokacin yana tsaye awajen yay folding hannunshi a kirji yana kallonta dan baya komi ga mamakinta saitaga ya sakin mata wani cute smile da sauri ta dauke kai tanaji kaman numfashinta zai dauke saikuma ta mike zumbur ta zagaya ta bayan kujerun dan bamataso taje takusa dashi tawuce tafita daga GOPD gabaki daya da saurinta hartana neman fadi, iskan daya bugeta yasa tasaki wani hadaddiyar ijiyan zuciya tasami wani dan dakali ta zauna, hango Baba yafito yana nemanta yasa ta tashi da sauri tai wajenshi yace "me kikeyi anan" murmushi ta kakalo tace "Baba bansan asibitin nan mutafi gida" magungunan ta yamika mata a leda babba, karba tayi yace "gasunan birjik kiyita sha dazaran kin fara ciwon mutafi" wajen machine dinshi sukayi yatada ya dauketa sai gida.

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design, graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number 07010439656 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._💫

_DISASTROUS LOVE_💫

_MASIFAFFIYAR SOYAYYA_

_THIS BOOK IS 500 IDAN KINASO PAY TO 3107021073 AISHA MUHAMMAD FIRST BANK, SAIKI TURO EVIDENCE OF PAYMENT TO MY WATSAPP NUMBER 07012181461_

✍🏾M SHAKUR

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design, graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number 07010439656 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._

EPISODE9️⃣

_FREE PAGE_

*****

Gidan nan babu wanda bai shigo yamata yajiki ba Maman Dady har wara takawo mata ma sabida ranan wara tayi ta karba cikeda kunya tamata godiya, Mama ma ba yabo ba fallasa tamata yajiki agaban Baba hakan yasa Baba yaji dadi, sanan yace taje ta kwanta adaki tahuta babu abinda zatayi yau shikuma Baba yawuce uwardaka wajen matarshi.

Da sallamaya shiga dakin zaune yaganta bakin gado tana fifita Abida datai bacci da mafici dan babu wuta tayi kyau sosai taci gayu tasa atamfarta mai kyau harda sarka awuya kaman wacce taje biki wanda abune dayasan bata sabayiba, zama yayi kusada ita tareda washe baki yace "wanan kwalliyan fa ni akamawa ne"? Wani banzan kallo ta jefeshi dashi sanan tace "kai asuwa, ni kaga dan Allah kabarni damuwan dake kaina daban Baban Habib" binta yayi da kallo yay shiru, dan yatsine fuska tayi saikuma ta nisa tace "uhm gwara ma nagaya maka, daga gidan Madam nake" yanda ya kalleta da sauri tareda sake natsuwa yasa ta gyadamai kai tace "gwarama kai salatin da kyau kaji, kirana tayi awaya tace nazo, nashirya naje nasameta tace min yaya ake ciki taji mijinta da mutanen nan namagana awaya ranan lahadi jibi kenan dan yau

ai Jumma'a zasuzo, wai ya mun shirya mun gama hada kudin nace mata ko asi bakada shi balle chasi" wani gumi Baba yashare ahankali yace "innalillahi wa innailaihi raji'un, wlh inda nasan haka abin nan zai kasance daban karba ba dukkece kika sani awanan ukuban" wani irin zaremai ido tayi tace "nice mene kace"? Kasa maimaita maganan yayi daya kalli kwayan idanunta saikuma ya saukar da murya ahankali yace "kiyakuri badake nakeba" kwafa tayi tace "Allah yasoka wlh dasaika raina kanka wlh mtswww" taja tsaki, ahankali yadafa kanshi saikuma ya buga tagumi saikuma ya kalleta cikeda damuwa yace "yaya zanyi yanzu Ruka kifadamin abinyi"? Shiru tayi tana kallonshi saikuma ta nisa tace "Mijin Madam yariga ya sanarda mu duk wasu ka'idoji da sharuddai na wanan lamarin ko kaje still maganardai itace zai sake maimaita maka, amman dudda haka yanzu katashi kaje kai wanka ka chanza kayan nan kasa wanan giznar danasa kasaya, ka feshe kanka da turare katafi chan sakateria office dinshi kasame shi kaje kuyi magana mai kyau, yafada maka idan dawata hanya dazakabi kome yagaya maka kadawo kasanar dani daga A zuwa Z sabida nasan yanda zamu bulloma lamarin daganan in lokacin Jumma'a yayi saika wuce kadawo gida karka biya ko'ina kadai jini ko" gyadamata kai yayi ta tashi tace "bari naje naduba ruwan dake murhu inyay sanyi kayi wanka da ruwan sanyi dan gaskiya sabida kai bazan hura wuta naci gayun nanba" tawuce tafita yabita da kallo yaji zafin yanda take gasamai magana amman yakasa cemata kala, kayan yacire yasa jallabiya yabi bayanta takaimai ruwan tadawo daki.

Fitowa yayi yadawo daki ya shirya tsaf yay mugun kyau kaganshi zaka dauka wani alhajine harda fesamai turare sanan tace "saura ka kalli wata mace" dan dariya yayi yaja hancinta yace "inada mace har mace irinki mezanyi da wata Ruka Baban Habib sai Maman Habib" murmushi tayi cikeda sonshi tace "nidai wuce katafi" tai maganan tana bashi key machine dinshi ta tasashi agaba har waje dudda yaso yama Fatima sallama dan taga yanda yake  kallon dakin but bata bashi damaba haka yaja machine yatafi, murmushi tace "kwanaki kadan yarage kurabu" tawuce takoma daki,  hijabi ta dauka tasaka sanan tafito ta shiga dakinsu Fatima, akwance ta ganta tana bacci, da kafa tasa  ta hambareta da sauri ta farka harara ta balla mata tace "tashi kifita falo kizauna kimin gadin Abida tana bacci nikuma zan fita, in yarana sun dawo daga boko ki basu abincin dana dafa yana kula" gyadamata kai tayi ahankali Mama taja tsaki tawuce tafice daga gidan.

Wuraren goma Baba yakai sakateria yana kaiwa gate yay parking mai gadi yace "wajen Oga Abdul kazo ko" dasauri Baba yace "eh" ciki mai gadi yayi saigashi yadawo yace "yace kashiga" wucewa ciki Baba yayi yay knocking gaban wani dan madaidaicin office daga ciki aka amsashi "shigo Malam Muhammad" bude kofa Baba yayi ya shiga wani mutumi ne yana sanye da suit zaune akan kujera daga ganinshi kasan ba bahaushe bane banufe ne ya fadada murmushin kan fuskarshi yace "barka da zuwa Malam Muhammad"  yamikama Baba hannu suka gaisa sosai sanan yakoma ya zauna yanuna ma Baba waje shima ya zauna sanan yace "ya ake ciki mutumina kahadama mutanen nan kudinsu kuwa"? Da sauri Baba ya girgiza kai anatse yace "saisa na shirya nazo wajenka Oga Abdu naga kana mutunci da mutanen nan saisa nazo ka taimakeni kadubi iyalina ka nemamin alfarma awajensu dan Allah, su dan karamin kwanaki zan

biya wlh, ka taimakamin" hmmmm Oga Abdul ya fuzarda iska sanan ya kalli Baba yace "Malam Muhammad kasandai kai mutumina ne ko kuma tsakanina dakai babu boye boye, babu karya kowani abu,  maganan gaskiya shine mutanen nan basusan menene alfarma ba wlh, saisa suke cewa mutum dakanshi yafadi yaushe zai biya back kuma duk ranan daya fadi ranan zai biya ko yabi sharadin daya yarda akai dazai ari kudin, mutumina idan baka da kudin nan bakada hanyar samu ka biyasu, kawai kabi  sharadin inba hakaba kasan sauran" shiru Baba yayi gabanshi nafaduwa sosai yama kasa magana hakan yasa Oga Abdul yace "kaima ka tafka kuskure anbaka makudan kudi haka dazasu chanza maka rayuwa ko gonace tunda daman shine sana'ar daka iya dakaje kayi amman bakayi ba kaje ka wulakantar da kudaden nan, kasai machine da sauran su kana washagali bakasan rana irin tayau zatazo ba gashinan idanunka sunyi ja" yay maganan cikin dan fushi dan Madam tagayamai abinda yayi da kudin ya chanza matarshi kayan daki da gida, ganin Baba yakasa magana saikuma yabashi tausayi hakan yasa yakai hannunshi yasaukar da hannun Baba daga kan kuncinshi dayay tagumi dashi yace "kaga abokina bashi kaci ba kisan kai kayiba, kowa nacin bashi,  abinda nakeso dakai kabasu dan naka kawai, d'ana yaje yay aikatau dasu, wanan sirri ne dabana fadima kowa, nima naci bashinsu nakasa biya dana yaje, basa wahalar da yaro, ba cuta ba cutarwa yaro yay aikinshi duk wata ana biyanshi a matsayin biyan bashinka, yarona yadawo na ganshi yamafi sanda yake gidana akarkashin kulawata kyau wallahi, kawai kabasu inbadai so kake adaureka agidan yari ba dan trust me mutanen nan sune hukuma gabaki daya wlh bazaka iyaja dasuba kokai waye I know what am saying, kawai ka shirya ranan lahadi by 9 tamaka a wanan hotel din dasuke sauka in sunzo katafi dayaronka kabasu baki alekum agabanka zasuyi documenting yaron sugaya maka salary shi dakuma aiki watanni ko shekarun dazai musu, kaikuma saika dage da nema kafin lokacin kahada kudin katura musu adawo maka da danka cikin lumana kaji ko" gyadamai kai kawai Baba yayi, nan Oga Abdul yacigaba da bashi shawarwari sanan wuraren daya suka fita tare zuwa sallan jumma'a daganan yawuto gida.

Da sallama yashigo falon Fatima yagani tana share falon dayay kaca kacha da abinci alamun yara sunci abinci, da sauri yace "inasu Habib da Sadiq dasukaci abincin suke dakike shara"? Mama ce tafito daga dakinta ranta abace tace "sun koma wajen aiki, Habib yatafi gareji, Sadiq na shagon dinkinsu, Ibrahim na wajen kafinta kagako tunda itace agida bata zuwa wajen aiki aisaitai sharan, wuce mutafi daki" tanunamai hanyar uwardaka, wucewa yayi itakuma ta watsama Fatima data cigaba da shara abinta harara sanan tashige dakin nasu, zaune taga Baba kan gado yacire riganshi yarataye a kofar sip yarage dagashi sai farar shimi da dogon wandon shaddan ya zauna, washemai baki Mama tayi tace "musamman nahada maka kunun aya mijin Ruka" tai maganan tana tafiya wajen wata yar karaman fridge dake uwardakan tabude taciro katuwar goran kunan Aya tadaura a tray da kopi tazo ta ijiye kan dadduman data shimfida a kasan uwar dakan sanan ta dauko kulan abincinshi takawo tazauna akan dadduman ta kallai tace "sauko" saukowa yayi ahankali tabude kula tana kokarin zubamai shinkafan data dafa yace "ina Abida?" "Uhm wanan rigimamman tana dakin su Habib tana bacci" janshi da hira tadinga yi yacinye abincin tass yasha kunun ayan dayay dadi sosai sama da rabin gora ya kalleta yace "ke

bakisha kunan ayan ba dukni na shanye" dan dariya tayi tace "wanan nakane special namaka ninasha nawa tareda yaranmu dazu, shanye kaji" daga goran yayi ya tsiyaye ragowan wanda yarage a cup yakai baki ya shanye tass wani irin murmushi tayi tace "haka nakeso yallabai, baka bani labari ba yakukayi da mijin Madam"? Danjim yayi for a moment harya manta saikuma yanzu yaji damuwan shi tadawo danya fall yanda yakasa magana yasa tace "ba gudu baja dabaya ko"? Gyadamata kai yayi ahankali, murya chan kasa tace "yanzu da gaske ranan lahadi Habib zaka dauka kaje kayi biyan bashi dashi"? Kallonta yayi yace "toya kikeso nayi eh Ruka? Kudinnan kinma finici aciki, kuma banda haka Oga Abdu yacemin basa cutarda yara ko kadan shima danshi yataba zuwa aikatau din daya dawo saima wani kara bulbul yayi, basaina bada Habib ba inyaso saina dage da neman kudi bada jimawa ba nasamu nahada nakai adawo dashi koya kikace" wani kallon raini tamai tace "kana haukane Baban Habib ko kanka yatabu ne dakake cewa zaka basu d'ana Habib"? Baki yabude zaiyi magana tawani dakamai tsawa tace "kamin shiru bance kai magana ba" hadiye maganan dazaiyi yayi kaman an daure bakinshi yana kallonta kaman d'a da Uwarshi.

Shiru tayi sanan ta kwalama Fatima kira."ke Zara'u" da sauri Fatima tafito daga dakinta tayi bakin kofarsu batare data daga labule ba ta tsaya awaje cikeda girmamawa tace "gani Mama" cikeda batarai da masifa tace "dau Abida ki goya ki tafi gidan kawarki Maryam karku dawo yanzu" abin bakaramin mamaki yabata ba yanda Mama da kanta tace tafita taje wajen Maryam, washe baki tayi cikeda jin dadi tace "tom nagode Mama" da sauri tajuya, Mama tace "saura inji kinbiya wani wajen jaka kawai mai kama da zabiyar dila" bata damuba ta goya Abida tasaka hijabi tafito tace "muntafi Mama" tsaki Mama taja bata bata amsaba tace "jamin kofar falo" jan kofar tayi, sanan Mama tajuyo ta kalli Baba ta gyara zama tace "dagani sai kai saikuma mahalliccinmu ne adakin nan Baban Habib, kalle ni nan ka kara ni dai Rukkaya matarka ko ana hamaza hamata wlh wlh, billahilazimu bazantaba bari kakai d'ana yaro karami dan shekara goma sha 12 chan wani garine ko kasane ohon musu aikatau ba da sunan biyan bashi ba kaji na rantse maka kuma kasan halina sarai basai anbaka labari ba" gyadamata kai Baba yayi kaman wani yaronta yace "shikenan abar zancen Habib zan samesu jibin nagaya musu bandashi inyaso dukma yanda zasuyi sai suyi" da sauri tace "hauka kake? So kake su kulleka? Ni zaka jama abin fadi aduniya ana ganina da daraja aji labarin an kullemin miji dama dukkudin damuke wasshagale dashi na bashi ne, karma kasake kayi tunanin nan kana jina ko" gyadamata kai yayi ahankali yace "toya kikeso muyi"? Wani hadadden makirin murmushi ta sakinmai takai hannu ta tabashi tace "yanzu kai magana mai kyau my handsome miji na dan baiwa shege gakadai talaka bako sisi amman Allah yamaka bindi" tanuna wajen wandonshi, yanda take murmushi yasa shima yasaki murmushi kaman wawa, daure fuska tayi tace "zancen kai Habib bashi, zancen a kulleka sabida baka da kudin biyan su babushi shima, kaga yarinyar nan data fita" tanunamai kofa da sauri ya kalli kofa dan baigane metake fadiba yace "wace yarinya"? Daure fuska tamau tayi tace "yarka Fatima Zara'unka da ita zakai biyan bashin nan Baban Habib"!!!!

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design,

graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number 07010439656 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

_NAKUSAN GAMA FREE PAGES, IF YOU WANT THIS NOVEL IS JUST 500, SEND 3107021073 AISHA MUHAMMAD FIRST BANK, SEND EVIDENCE OF PAYMENT TO MY WATSAPP NUMBER 07012181461 THANK YOU_

✍🏾 M SHAKUR

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design, graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number takira 07010439656 , sanan zaki samesu a watsapp ta wanan number 08106788714 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._

EPISODE 🔟 &1️⃣1️⃣
_FREE PAGE_
Dawani irin sauri Baba ya kalleta yanda gabanshi yafadi har ita saida tagani, itama kureshi tai da ido kur tayi irin da magana ne amman yakasa furta uppan  saima ya sunnar da kanshi kasa, wani takadirin murmushi tayi tace "aina zaci zakace wani abune" tadanyi shiru tace "Fatima itace yarinya babban damukeda shi maidan hankali kuma yarinyar nan zata iya komi tarufa maka asiri, ta mallaki hankalin kanta shekaranta sha tara duk inda muka kaita hankalinmu akwance sabida musan zata kare kanta" ahankali kaman wanda ke tsoron magana yace "Ruka mutanen nan kin manta sharadinne yaro namiji kadai suke karba basu karban mace" dan dariya tayi tace "ance maka ni dakikiyace irinka hmmmm" tadan girgixa kai sanan tace "inada plan, hadaddiyar plan" ahankali bakinshi har rawa yake yace "wani irin plan?" Murmushi tayi tace "zamu komar da ita namijii"!!!! Zuru zuru yayi yana kallonta kaman sauna ta gyadamai kai tace "zamu komarda ita namiji ta hanyar boye duka hallitun mace da Allah yamata Madam cema tabani shawaran nan dan itama tasan Habib yay karami ga Habib ba wayau, inada wasu kudi dubu goma zan ara maka gobe zan shiga kasuwa, zan sayo silkin doki dashi zamu kulle mata kirji wanan manyan maman datake dashi dauresu zamuyi tamau, kanta ko nida kaina yauzan zauna namata zane yan kanana zan sayo Bald cap (hulan fata na kwaiwaido) zan zauna nasaka matashi da gam, sanan zan sayo kayan maza riguma da wando na gwanjo burguza burguza dakuma Ghana masgo, hujin kunenta  akwai wata yar fata dazan like awajen baza'a taba gane antaba huji awajenba saikuma takalmi kito, da kambas, wanan maganan dagani sai kai da madam da mijinta, duk wanda yatambayi Faty zakace tayi tafiya ta tafi wajen Baabarta na Abuja hatta su Habib bazasu sani ba kanajina" gyadamata kai yayi kaman maraya, hararan shi tayi tace "duk duniyan nan bakada mace mai sonka maikuma rufamaka asiri irina dan haka kadinga godemin, kuma bayau zaka sanarda Fatima ba sai gobe sanan agabana za'ai komi kanajina ko" gyadamata kai yasakeyi kaman maraya yakasa magana yakuma rasa abinda yasa yakasa magana, murmushi tayi har cikin ranta ganin yanda maganin sabon wajen da Madam ta kaita yay aiki sama dana tsohon datake amfani dashi da, murmushi tayi tabudemai hannayenta tace "zonan mijina" da saurinshi da rarrafe yashiga jikinta ta rungumeshi tana shafamai baya tace "inhar kanajin maganata kanamin biyayya bakada matsala wlh, komenene zan tsayamaka aduniyan nan, duk rashin kudinka ina sonka, ni bankibama kai zamanka agidaba nina dinga fita nema dan wlh banson mata na kallemin kai kafin wata ta kyatsa amin wuff dakai dole na tsaya tsayin daka aranka, dan kyakkyawan bafulatanina" ta shiga sarrafa shi wai ance duk wayan namiji yashiga hannun mace jariri yake dawowa, shida kecikin damuwa dayake rikakkiyar yar tasha ya aura tuni ta mantar dashi tana tsotse shi saigashi yafara ihu suka shiga cin juna yau harda ihauce ihauce barinma shi dayajita yau daban saida ta taushemI baki sabida ihun yasoma yawa sai sama Madam albarka take yanda taga lokaci daya Baban Habib ya susuce mata ba ita tabarshi ba sai wuraren karfe biyar daga ita harshi sun galabaita da kyar ta sauka ta zura hijabi tayi tsakar gida tana taku dai dai madam tafito yar gatan mijinta tawuce takaimai ruwa bayi sukuma suna gulman su Kullum yana gindin mace an maidashi sauna sai yanda akai

dashi.

*********

"Kewai mesa yar kauyece Zara"? Cewan Maryam da tundazu suke hira da Zara datazo tana bata labarin rashin lafiyan datayi just this two days, Abida kuma nachan dakin Maman su Maryam tanacin tuwon da aka dafa tana wasa.
Hararanta Fatima tayi tace "ni wlh ko kallonshi nayi sai gabana yayta faduwa" wani irin dariya Maryam tashigayi tafada kan yar yaloluwan katifarta tana daga kafa, daure fuska Fatima tayi tace "me haka wanan dariyan fa"? Da sauri Maryam ta tashi ta zauna tace "ke wlh sonshi kike" da sauri Fatima ta zaro idanu cikeda wani irin mugun mamaki gyadamata kai Maryam tayi cikeda jinjinawa tace "eh ke matsalata dake baki karance karancen littatafan soyayyane dakin gane menake fadi, kinsan ko ance duk namijin dazaka gani gabanka yayta fadi shine zaka aura ko shine mijinka" wani irin kallonta Fatima take kaman tasami TV, Maryam tace "kuma shima wlh sonki yake, har yana barin aikin dayakeyi yazo yatareki dankarki fadi kice kaza kaza, ina gayamiki sonki yake kawai dai bai sami ta hanyar dazai fadimiki baneba kawai, kuma zakigani nan....." da sauri Fatima ta tareta tace "ni mubar maganan dan Allah  banmaso wlh meneke dashi da irin wanan mutumin zaiso mace kaman ni ke kinganshi ne kuwa? Hanyar jirgi daban hanyar mota ma daban abar maganan" tashi Maryam tayi tace "anbarta bari naje na dauro alwala nai salla gwara ke aurenki da gata for now Allah ya yafemiki" murmushi tayi saikuma tamata gwalo irineh din jedai kiyi, Maryam tafice daga dakin tana dariya tace "dadin abin nimadai nakusan zuwa nawa hutun sallan" samin kanta tayi da tunanin maganganun Maryam saikuma tai maza ta kawarda zancen daga zuciyanta,  ranan wuni tayi tareda Maryam har Magrib itama Abida batai kukaba dan tasami tuwo taci takoshi tai nak sai wasa take abinta sunama Maman su Maryam barna adaki itada kannin Maryam, koda takoma gida taga Baba na nan baifita ba suna hira shida Mama ta gaidasu Mama ta dauki Abida itakuma tawuce daki.

Washegari Asabar batabar Baba yaje ko'ina ba bamata barshi ya zauna shi kadaiba sabida batason yay tunanin abin, sai wajajen 9 nasafe suka fita ita dashi sukai kasuwa tare suka sayo kayan gwanjo riguna masu kyau kala biyar dogayen wanduna jean burguza burguza kala biyar, sai kito sabo da cambas na gwanjo guda daya, da ganamasgo da fatar kwaikwadon kan Bald cap, da fatan kunne da silkin dokin dakomima sanan suka dawo gida wajajen karfe daya suka shiga uwardakan su da kayan bata bari Baba yaje mallaci ba sukai salla adaki already yara duk sun dawo gida since abincin rana sukaci suka koma aiki, saida sukaci abincin da Fatima takawo musu sanan Mama ta kalleshi tace "lokaci yayi kira yarka muyi maganar anan uwar dakana" gyadamata kai yayi abin tausayi muryanshi har wata yar dishewa tayi ya kwalamata kira.

"Za.....Zara, Zara'u, Zara" dag daki ta amsa da "na'am Baba" fitowa tayi tazo ta tsaya agaban dakin batare data shigoba ahankali yace "shigo" sallama tayi ta shiga dakin tasami waje tabakin kofan ta zauna akasa tace "gani Baba" shiru yayi yana kallonta duka duka yaushe yarinyar nan taji sauki dahar zai iya mata wanan maganan ganin yakasa magana sai kallon yarinyar yake kaman yauya fara ganinta yasa Mama ta kalli yarinyar tace "Fatima ayanda mahaifinki yawahala dake aduniyan nan inhar kika kasa rufamai asiri awanan bakin yanayi dayake ciki wlh sai Allah yay mummunan ykamaki, tun kina yar shekaru biyu mutumin nan yake wahala danya sami kudi yaciyar dake" Mama tai shiru tana kallon Fatiman dataga bata gane komiba kan zancen datake fadi, Mama tace "lokacin dakika gama Js3, zaki shiga SS1 wato shekaru uku kenan dasuka wuce lokacin muna wanan tsohon gidan damuke ada, Babanki fatara ta isheshi baida hanyan samin kudi yasakaki a school gashi har anfara first term kina zaune damu agida, wata kawata mai suna Razika tare muka taso tai aure mijinta Lawyer ne amman karamin lawyer yana kiranta da Madam hakan yasa sunan yabita, muna cemata madam, akwai wasu lauyoyi da mijinta kema aiki, suna taimakama musulmai ta hanyar basu bashi kona miliyan nawa kakeso kekona biliyan nema zasu baki sanan babu interest, ayanda suka baki kudinsu ahaka zaki mayarmusu dashi batare dakin kara musu ko ficika ba, su kalan tasu yanayin taimakon kenan, sanan idan kika karba keda kanki zaki fadi ko shekara nawa, wata nawa koma dai yaushe kikeso ki biyasu kudinsu bak sharadin dayane duk randa kika fadi zaki biya back ranan zaki biya, idan ranan tazo baki dashi akwai abu biyu kodai su kulleka agidan yari kokuma kabada danka namiji babba yaje yamusu aiki zasuyi calculating sufadi maka albashin danka misali suce alabashin yaronka dubu dari duk wata to haka yaron zaiyi aiki harna watananin dazai daukeka kudin dasukebin ubanka yakare, but duk randa uban yasami kudin zai iya kiransu yabasu adawo maka da danka cikin koshin lafiya, danaji wanan labari mai kyau dan tunda nake arayuwata ban tabajin wanan kalan taimakon alheri hakaba, aduniyan nan yanzu ko kawarka tabaka aron kudi saita cemiki idan kin juya zaki dawo mata dashi ki kara mata wani abu akai, amman wanan kam ga makudan kudi ko nawa kakeso sanan kaida kanka zaka fadi ranan dazaka biyasu back babu ko anini asaman kudin da gudu nadawo na sanarda mahaifinki duk wanan bayanin dana miki nidashi muka shirya na kaishi wajen mijin madam Oga Abdu, yamana hanya dan irin kudin nan sai kanada hanya kanada kafa, yamana hanya aka saka sunanshi cikin masu neman bashi akace za'a nemeshi I, bayan kwana bakwai aka kira babanki aka dauki information dinshi, Mijin Madam ya tsayama Babanki amatsayin guarantor na Babanki kuma witness na babanki dan bansan kowa yasani asan bashi mukaci, aka kirga miliyan uku cash yan sababbin dubu dubu aka bama babanki yadawo da miliyan uku cash a hannu gida, kafin yadawo bayan anbashi kudin yarikesu a hannu aka tambayeshi yaushe zai biyasu instead yace shekara goma ko shekara ishirin ma bayaga miliyan ukuba sai kawai yafurta shekara uku shima kaman wawa yadawo gida yake gayamin shekara uku yace kinga fadan dana mishi saikuma na share muka biyamiki kudin makaranta kika fara ss1, kanenki ma haka, muka chanza gida, yasai machine ya gayaramana daki yasai mana katifu kujeru da komidai dakika gani na wanan dakin ahaka kudi suka kare wanda har yau dadan ragowan chanjin muke rayuwa yanzu haka gobe ne ranan biyan bashi ko bada d'a Fatima ko akulleshi, ke yarinya ce Fatima mai basira ilimi dakuma fikra kinsan Habib yay karanta daza'a kaishi aikatau, Habib baidama hankali balle ya tsare kanshi saisa ubanki ya yanke shawaran kezaikai amman zamu maidake namiji" tunda Mama tafara maganan kanta akasa sai alokacin ta dago kanta ta kalli Mama shima Baba ita ya

kalla sabida shairin dayaji tamai, wani mugun kallo tama Fatima tace "kobazaki rufama mahaifin naki asiri bane butulu? Dakuma nace maidake namiji ba ina nufin nane miki tsuliya ko yanke miki mama nake magana ba a'a zadai mu boye hallitunkine, ga kayan damuka siyomiki nan na maza" tanuna mata ganamasgon sanan tace "ke kinsan bantaba miki karya ba, inhar baki yardaba kulle ubanki za'ayi kuma kinsan mahaifinki baida kowa dazai iya biyamai miliyan ukun nan, saidai agana mishi azaba agidan yari karshenta ma akashe shi achan, kafin yay signing duk angayamai sharuddan nan kuma ya yarda ya amsa, idan yanzu suka tafi dake aikatau din zai dage da nema Oga Abdu yamin alkawari zai samomai aiki dudda baiyi makaranta sosai ba zamu dage nima zan fara sana'a cikin wata biyu ko uku mubiya mu madawo dake, zaki iya hakuri kiyi rayuwa namiji ki boye macen ki aciki na watanni dabasufi uku ba dan rufama wanan mahaifin naki daya miki komi asiri? Mahaifinki dake wahala dake tun kina yar tatsitsiya ya raineki shi kadai mutuminnan, yay achaba, yay faskare, yay leburanci duk sabida ke, yanzu lokaci yayi dazaki nuna mishi baiyi haihuwan banzaba kema yar halak ce zaki iya"? Ahankali ta kalli Baba dataga kanshi akasa dan hakanan yaji ayau yana kunyar yarshi bai chanchanci zama mahaifinta ba, tuna tun tana yarinya yanda yake wahala da ita tayi da wanan rashin lafiyan datayi, dakuma yanda yakeda hawan jini, aduniyan nan da'a kulle mahaifinta gwara an kulleta so dubu, da mahaifinta ya tozarta aduniyan nan gwara ta to tozarta sau dubu, da'aci mutuncin Abban ta gwara acinci nata, da ubanta yamutu gwara ita ta mutu, da Baba yasha wahala gwara tasha wahala. Cikin fushi Mama tace "kinmin shiru" ahankali takai hannu ta goge hawayen dasuka zubo mata tace "Mama babu abinda bazan iyama Abbana ba koma menene aduniyan nan, zanje zanyi aikatau din koda Baba bai sami kudiba zanyi aikin koma na tsawon shekara nawane dazai dauka bashin yakare, Baba kadena damuwa kaji karka fara ciwo" tai maganan ahankali tana kallon Baba dayaji jikinshi yadawo kaman kankara, wani hadadden murmushi Mama tayi tace "kaga yarinya yar albarka maison mahaifinta, duk diyar data rufama iyayenta asiri Allah zai rufa mata itama, cikin dare zan tadake na shiryaki anjima zamuyi kitso, dau kayan gwanjon kije ki wanke kinji ki shanya su bushe yauko mekikeso ninezan dafamiki dakaina yar albarka, me zakici"? Murmushi ta kakalo ta girgiza kanta tace "bakomi" cikeda farinciki Mama tace "ai ina saina saimiki tsiren dare yau" daukan ganamasgon tayi tafita dashi kayan tacire tadau omo ta tafi makwarara wanki, Mama ta kalli Baba dahar lokacin kanshi akasa tace "dalla me haka sokake tadauka akwai wani abu akasa ne iyye saki ranka jor mutuwa zatayi komene nifa banson haka, tashi kahau gado muyi baccin rana" tashi yayi yahau gado haka dan dolenshi tasashi yay bacci.

Wanke kayan tayi tass tana kallonsu itace yanzu zatasa wanan kayan mazan wandunan ma kaman sun mata tsawo dayawa, komawa tayi daki ta zauna, itakuma Mama saida ta tabbatar Baba yay bacci sanan tafito tace "xomuyi kitson" babu musgunawa haka Mama ta zauna ta zuba mata zane yan kanana masu kyau gashi har tsakiyan bayanta data gama ta tupke bakin gashin tace "cikin dare zamusa hulan fatan, nasiya miki always dayawa zan saka miki a kasan jakan duk wata karki bari kowa yasan kinayi kitafi da magungunan ciwon mara karki sake kibari asirinki yatonu dan kashe babanki za'ayi kinga yanda baida lafiya hawan jini yamai raga raga" kaman ba Maman data sabada itaba yau tsabagen dadi zama tayi tana koyama Fatima duk yanda zatayi harda koyamata muryan dazata dinga yi da kalan tafiya dakomima ranan bata bari

tai girki ba ita tayi.

Cikin dare Mama tashigo ta tadata ahankali gudun karsu tada yara fitowa falo sukayi Mama ta zaunar da ita, tasanya mata bald cap dinan bayan ta zuba gum da ake sa bald din dashi ta shigar da gashinta tass ciki abin yabame bam gashi tasayo daidai kalanta fari sabida farace, kan yay kato amman ba chan chan ba, sanan tasamata fatar daya rufe hujinn kunnenta shima, cikedajin dadi Mama tace "tashi ki kalli kanki a madubi" ahankali ta tashi taje ta tsaya gaban madubin falonsu tana kallon kanta badadan atampan dake jikinta ba zaka rantse namiji ce ita, ahankali tadaura hannunta ta shafa saikon kannata hawaye taji zasu zubomata hango Baba datayi ta madubi yafito ya tsaya abakin kofa ya rungume hannunshi yana kallonta yasa tahadiye kukan tajuyo tareda  murmushi tace "Mama yay kyau nayi kaman Habib ko" dan dariya Mama tayi tamika mata kallabinta tace "ungo daura karki bari su Habib suga kan, da sassafe gobe zan kadasu hadda karfe tara zaku tafi keda Babanki jekiyi kwanciyarki" wucewa tayi ta shige dakinsu itakuma Mama ta watsamai harara tace "wuce ciki" ciki yayi ba musu, daren cikinsu babu wanda ya runtsa ita Mama farin ciki yahanata Bacci zata rabu da ƙaya Allah yayi fatanta Allah sa nan gaba agane mace ce asirinta yatonu su kasheta tahuta gaba daya dan ta tsani yarinyar nan, Baba kuma damuwa ainun yasan yacuci yarshi sosai, guilt yahanashi ya runtsa, itakuma Fatima kuka tayi sosai na tausayin Babanta yanzu bazata gansu ba sainan da wata uku, tana tausayin Babanta sosai tana addu'a Allah yabashi aikin yi sabida karyaje yasake karbo wani bashi dazai sakashi a matsala irin wanan.

Tun karfe biyar Mama ta tashi tadaura girki tana gamawa ta tadasu Habib tamusu wanka, kowa yafito yay wanka bakwai daidai ta kadasu babu yanda sukaso suka tafi haddan tun kafin 8, tacema Fatima taje tai wanka wanka tafitayi hakan yabata daman balbale Baba da masifa kan yasaki ranshi, hakuri yabata sanan ta barshi Fatima nafitowa daga wanka Mama tabita dakinsu.

Yau duk yanda takejin kunya saida Mama taganin mata nono, silkin doki Mama ta dauka da akama igiya ta bakunan guda biyu tace "kullum wanan zaki dinga daure nonon ki dashi sabida kar agansu" nannada mata tayi sanan ta daure tamau harsaida tai yar kara sabida azaba takasa tsayuwa da kyau, Mama tace  "ahaka zaki rufama baban naki asiri tsaya da kyau jor" tsayawa tayi da kyau da kyar Mama tace "sannu duk idan zakiyi bacci kidinga kwancewa kadan" sanan tabata singileti tasaka sanan takawo rigan mazan navy blue shirt mai gajeren hannu tasaka Mama ta kulla boturin ba laifi nonon sundan boye sabida rigan dama burgujeje ne baka ganinsu sanan tasaka Jean din daya mata yawa mama ta nannade kafan suka kama kwankwason jeans din da igiya, sanan Mama tabata kamvas tasaka, Mama takoma baya ta kalleta batada banbanci da namiji kaman irin yaran nan maza da yanzu suka fara balaga dinan,

kawai kyaune da ita sosai ga pink lips na bala'i which is normal daman sunsan babanta kakkyawa ne jini fulani da buzu ce yarinyar,  ran Mama shar ta kwalama Baba kira tace "zokaga diyarka" shigowa dakin yayi shima ya shirya kallo daya yamata yadauke kai yawuce yafita, Mama tace "yanzu saka hijabi sabida kar yan gidanku su gane sai kunyi nisa sosai saiku cire babanki ya karba yaboye" hijabinta tasaka har kasa, Mama tahada mata jakanta fess saikuma tabata jakan goyon makarantan Habib tazuba mata abinci a flask tasa mata cinyan kaza da biskit guda biyu, da ruwan gora dakuma lakasera guda daya, karba tayi tana godiya, Mama ta kalli Baba daya zauna tace "tashi kutafi takwas da rabi" tashi yayi yawuce yafita Mama bata damuba tadau jakan tarike suka fito ta kwalama yan gidan kira tace "Fatima zataje hutu wajen Baabarta" sallama suka mata Maman Dady tabata 200 suka mata rakiya har waje, Baba yajuyo yana kallonsu agaban machin tasamai gana masgon itakuma tahau baya tana rikeda jakan Baba yatada machine din suka tafi.

Tafiya mai nisa sosai sukayi kasancewa hotel din dazasu da nisa dan hanya fita daga kano ne, sunyi tafiya mai mugun nisa sanan yay parking akan hanya ya sauka itama ta sauka hannunta yarike suka shiga wani uncompleted building dake kan hanyar har lokacin yakasaa kallonta, suna shiga ta kallai ahankali tace "Baba hijabin ko"? Da sauri ya gyada matakai yana juyamata baya, ahankali tacire hijabin tarike a hannu tana kallon bayanshi tasan yadamu hakan yasa ahankali tazagaya ta gabanshi ta kalleshi gani tayi idanunshi sunyi jajir kaman wuta, ahankali tace "Baba menene?" Kaman jira yake saukar da guiwowinshi yayi kasa  ya rike hannuwanta biyu fuskarshi yadaura kan kafafunta baitaba kuka ko hawaye gaban yaranshi ba amman wanan karan yakasa daurewa saiga hawaye sharrr da sauri ta zube akasa itama ganin fuskarshi da hawaye yana kuka yasa tafashe da kuka sosai zatai magana yadaura hannunshi kan bakinta cikin wata irin murya mai rauni sosai yace "Fatimatul Zara'u kiyafeni, ki gafarceni, ki yafema mahaifinki,  tunda na haifeki baki tabajin dadina aduniyan nanba, niba uba nagari bane, jibi abinda nasa kika zama, namaidake namiji sabida kawai na rufama kaina asiri, Fatima na cutardake dayawa aduniyan nan, dan Allah kiyafemin, kiyafema Babanki" wani irin kuka takeyi tashiga girgizamai kai tace "Baba kaine uba nagari dana sani aduniyan nan, da ace akwai wata rayuwa bayan wanan still kai zan zaba kazamto mahaifina Baba, kaizan saba danni kaina nasan I am so lucky da Allah yabani kai amatsayin ubana, Baba dan Allah kayakuri kadena kuka, bakamin komiba kaji, koma kamin nayafe maka duniya walahira nima kayafemin Baba" kamota kawai yayi yarungumeta tafashe da kuka sosai ajikinshi ta kankameshi dan yasa taji wani iri yanda taga Babanta nakuka, sun dade sosai ahaka sanan tace "Baba tashi mutafi zamuyi latti" tana maganan wayanshi na ringing sakinta yayi yana duba wayan yaga Oga Abdul ne bai daukaba ya maida aljihu yatashi tareda karban hijabin ya share mata fuska sanan ya ijiye hijabin awajen suka fito yahau machine itama tahau yatada suka shiga titi, tunda tai wayau bata taba fita ba hijabi ba ballema har ba dan
Kwali yau itace iska ke daka yana ratsa tundaga kanta, kunnuwanta da wuyanta haka, haka suka karasa hotel din mai suna Prestigious, yana shiga yaga Oga Abdul yaci suit sai kallon agogon dake daure a hannunshi yake, yana ganinsu yataho dagudu murya chan kasa yace "kayi latti sosai sokake kasamu a amtsala" ya kalli Fateema yace "good, from now sunanki

Khalid understood" gyadamai kai tayi, yace "any question dasuka miki answer them da turenci, sukaga u are educated zasu yanka miki albashi mai yawa nan da nan agama biyan bashin babanki" tasake gyadamai kai, ya shiga gabansu da saurin shi yace "let's go" jikinshi har rawa yake hakan yasa taji gabanta na dukan uku uku, shiga hotel din sukayi sukai upstairs, wani babban hall suka shiga ga security guards gardawa aciki, hall ne da aka jera kujeru hadaddun gaske, ga maza manya magidanta amman irin talakawan nan haka kusan su 100+, ga yara samari maza agefe dabazasu wuce sa'oninta ba zuwa yan 22yrs suma zaune kan kujeru adayan bangaren kusan su 63 ko morethan ma, saikan hadadden stage din da akai decorating da flowers aka zuba wasu arnayen kujeru wasu hadaddun manya manyan lawyers ne da baristoci sunci suit suna rubuce rubuce ga laptops agaban su, da printers, kallon Baba Oga Abdul yayi yace "kujirani anan lemme talk to them nazo dan ankira sunanka yafi sau uku" stage din yayi zuwa wajen wani babban Barrister dan tsoho nema dukawa yayi yamai magana a kunne sanan yadawo yaje wajensu Baba kujera yanuna musu yace "kazauna za'a kiraku" zama Baba yayi yana rikeda hannun Fatima itama ta zauna a kujeran kusada shi, saishima Oga Abdul yazauna kusada Baba yace "yanzu nan police suka tafi dawani mutumi thank God kayi tunani mai kyau da....." "Muhammad Alhasan Muhammad" shiru Oga Abdul yayi jin ankira Baba, faduwa gaban Baba yayi haka itama Fatima dan yanzu saitaji tanajin tsoro sosai dan ga dukkan alamu wanan babban organization ne baba yaci kudinsu duk azatonta tazaci is just a small something, hannun Fatima yarike sukai stage, cikeda girmamawa ya gaida lawyoyin da duk suka zubamai ido suna kallon yanda danshi yay kama dashi, yace "yallabai bangama hada kudin ba amman ga......" kafin yagama maganan Barrister ya kalli Fatima yana gyara glasses din idanunshi yace "young Man akwai turenci" gyadamai Fatima tayi ahankali, yace "whats your name" gyara muryanta tayi ba yabo ba fallasa dudda muryam baiyi kaman na namiji ba hakama baiyi kaman na mace ba tace "ahhhm Khalid Muhammad" ajiyan zuciya Oga Abdul ya sauke, Barrister yace "how old are you"? Anatse tace "i am 19yrs old" documenting sukayi sanan yace "what level are you in school" ahankali tace "I just write waec this year" gyadamai kai yayi yace "what are you good at Khalid? What can you do what are your skills?" Shiru tayi saikuma ta kalli Baba taga kanshi na kasa sanan takalli Barrister tace "only house work" da sauri Barrister yace "don't you go to work" gyadamai kai tayi tace "only school and islamiyya i go" gyadakai yayi cikeda gamsuwa dan yaga yaron na kokari turenci shi dai ba laifi normal turenci yaro dan arewa dayaje school, juyawa yayi ya karbi wani bracelet dataga anciro daga wani akwati an rubuta 65 ajiki yace "give me your hand" bashi hannunta tayi ya nada mata bracelet din sanan yakalli Baba yace "because your son is educated and can communicate da English, salary dinshi every month will be 120,000 naira, yakama zaimana aikin watanni ashirin da biyar (25) shekara biyu da wata daya kenan" ya kalli Fatima da gabanta ke wani irin mummunan faduwa yanuna mata bangaren yaran yace "go and sit there with your mate, Abdul take her luggage to the car" gana masgonta Oga Abdul yafita dashi aka nunama Abba wajen zaman manya yawuce yaje ya zauna yakasa dagokai.

Wuraren 12 suka gama, sanan aka shigo da abainci yaran aka rabamawa hadadden fried rice da chicken da salad da ruwa da juice Barrister yace "eat Boys" yara sai dadi sukeji ganin abincin da basaci agida nan da nan suka cika hall din da hayaniya sanan akai dismissing iyayen su, security guards na fitarda su suka fara fita, da sauri tadaga kai ta kalli Baba kin

kallonta yayi harya fita tareda Oga Abdu yaki juyowa ya kalleta saidai yana tafiya ahankali kaman baida jini ajiki, ahankali taji hawaye yazubo mata kaman daga sama taji an rungumota takafad. "Dalla karkai kuka saikace wani mace eh guy" da sauri ta daga kanta wani saurayi tagani dabazai wuce 20 ba yana sanye da riga da wando shima kabar da hannunshi tayi cikin sabon muryanta tace "dalla malam karka kara tabani" taja kujeran ta ta matsar tabude jakan bayanta tasa takeaway aciki ta ijiye jakan akasa ta kafa fuskarta akan kafafunta kawai ta shiga kuka mai taba zuciya.

_MBM ENTERPRISE company ne mai zaman kanshi that are into anything computer design, graphics design, sunayin ID card, folder, files, meo, baje, sunayin jotter na biki da sauransu, sunayin customize mug da magic mug, sunayin jacket da riguna signout irin idan kun gama school, sunayin invitation card, sunayin p-caps, sunayin throw pillows da sauran su, sunayin calendar na turenci dana larabci, dakomima har kwalaye sunayi, ko'ina kake zasu maka su aikamaka dashi, suna logo creation, suna customized links, flash da souvenirs na biki na birthday na suna daza'a lika suayenku ajiki, sunayin receipt, gift box na birthday koma na menene, jama'a bari kuji indai design ne da ake amfani da kwamputa ayi to MBM Enterprise kaman sunmiki sun gama, har award sunayi, customize umbrella, key holder banda haka all services dinsu are at a very low discount rate, super affordable, idan zaki tuntubesu zaki samesu awanan number takira 07010439656 , sanan zaki samesu a watsapp ta wanan number 08106788714 kuyi saving ku musu magana ko a watsapp kokuma ku kirasu awaya._

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

✍🏾M SHAKUR

EPISODE1️⃣2️⃣
_FREE PAGE_

Sauran yaranne sukahau dariya though not all dan wasuma sunyi shiru sun natsu daga gani suna kewan iyayensu, shikuma yaron wani hararan shi yayi yafaracin abincishi kawai, takai kusan 20min ahaka, sanan ta tashi tagoge fuskarta tas da idanunta tass, ahankali taduka tadau jakan budewa tayi tadauki takeaway ta tabude ahankali tashiga turama kanta abincin sanan ta ijiye acikin jaka duk suna zaune wajen su kadai sai hayaniya yaran suke har wajajen karfe uku sanan securities suka shigo sukace "kutashi kuyi layi masu son amfani da bayi suyi, ga bayi nan anbude muku night journey zakuyi so get ready, prepare use 10min to do everything" bayika hudu dake dankareren hall din suka bude musu, ahankali ta tashi ta goya jakanta tai hanyar bayin wasuma nabinta abaya, shiga daya daga cikin bayinka tayi tarufe harda key sanan ta tsaya ta kalli kanta really fa batada banbanci da namiji da sauri ta dauke idanunta daga madubi dan bataso tana kallon kanta, fitsari tayi kaman tasani ta soke wani pad a aljihun wando dudda bata wani heavy flow dan gobenema zata gama amman saida ta dauka wanan dataji night journey zasuyi yasa ta chanza ta gyara kanta tareda flushing old one din ta shirya tsaf sanan tafito goyeda jakanta, tana fitowa security yanunata yace "kai kagama?" Gyadamai kai yayi hakan yasa security yanuna mai kofa yace "jemota ajeraku" fita yayi ahankali ya sauka kasa tareda wasu yaran, wani babban luxurious bus tagani kaman irin nasu landstar wanan hadadden bala'i kaman ma sabo, security dake tsaye gaban mota yace "oya zoka shiga" karasawa tayi ahankali ta taka tahau motan wani sanyi ne taji motar ga dankareren tv a kunne ga sanyi ga labulaye, security dake tsaye a tsakiyan motarne yana nunama kowa inda zai zauna yanuna mata sit yace "jeka zauna achan" karasawa tayi ahankali ta zauna kusada window, wani yaro aka turo yazauna kusa da ita dan sit bibbiyune jere akowani side, kafin agama jerasu tass karfe hudu, sanan taga wanan babban lawyer dayasa mata bracelet yana magana da security dukansu su biyar yabasu kudi wrapper yan dubu guda biyu har kasa suka duka sunamai godiya suna Allah iso dasu lafiya gobe da alamu su flight zasubi sanan dukansu biyardin suka shigo motan, daya ya zauna mazaunin direba, daya adayan bangaren mataimakin direba, sai uku suka zauna a first row na bayan direba dabasu saka any of the children akaiba, sanan suka tada motar suna dagama Barrister hannu harsuka fita daga hotel din suka dauki hanyar barin kano motar yay tsit sai securities din dake hira abinsu.

Ahankali ta lumshe ido azuciyanta tace "ina zaki Fatima Zarah? Wani kasa ko gari za'a kaiki? Nazaci anan kano zanyi aikatau amman wanan damuke barin garin kano ina zamu? Yau nice nake rayuwa amatsayin namiji ina amsa sunan Khalid, yau nine nake wani wuri da babu halitta daya dana sani, nine bana tareda mahaifina ko kannaina, nine nake barin garin danake zuea wani wuri daban ma saniba, Ya Allah kaga zuciyata Alkhairi nake nufima mahaifina Ya Allah na fawwala maka al amarina da rayuwata gabaki daya Ya Allah ka kareni ka tsareni, I am so scared, har kasan zuciyana inaji dabanyi wanan abinba amman kuma har kasan zuciyana inaji zan iya mutuwa aka kullemin Baba" hawaye ta share ta kalli gefe tadan bude labulen window ta kadan tana kallon hanya, itadai tunda take da wayonta bata taba tafiya tabar kano ba amman wanan tafiyan da ake motarsu na famfala uban gudu tasan

Kano zasu bari,  idanunta biyu harsuka fita daga kano suka kai zaria suka isa kaduna harsuka dauki hanyar Abuja lokacin dare yasoma yi, ganin tafarajin yunwa yasa tabude jakanta tasauki abincin taci takoshi tasha ruwa sanan ta ijiye ta gyara zama tadan saci kallon yaran dake gefenta taga shi yamayi bacci, hakan yasa ta zubama TV dake aiki a motar ido tana kallon film din da akeyi nafada, ahaka wuraren goma nadare bacci yay awon gaba da ita.

********

Har gaban gidansu Taxi yay parking lokacin duka duka baifi 10min tafarka ba dan alluran 6hrs ne, yabiya taxi yadauketa ya shiga cikin gidansu da ita, kofar flat dinsu yabude ya shiga da ita ciki da sauri kannenshi duka na falo suna kallo, dawani irin sauri yace "Ray yana get me a stethoscope daga dakina run" dagudu tafita, yace "Rahma get me ice" sanan ya kwantar da ita akasa, ya wurgan dakomi na hannunshi ganin 10min yawuce bata farka ba inbai tadataba zata iya rasa rayuwanta gabaki daya, sanan ya nannade hannun riganshi sama ya kalli Asma yake tsaye yace "fold this hand for me" linke hannun rigan tamai, sanan yadaura hannunshi akan kirjinta ya danne sau uku babu motsi bata farka ba, dasauri yafara no no no Fatima wake up, wake up, yanda yake ihu yasa Ammi dake sama tana hira da Maman mijinta data iso yau daga UK tadan zabura, tace "Granny kaman muryan Imamu nakeji" Matan da aka kirada granny wacce ta manyanta sosai amman kudi yasa bazaka taba ganewa ba, tahadu sosai tana sanye da glasses a idanunta hannunta rikeda supplement na diabetes tace "Imamu kuwa" "Fatima wake up!!" Wanan karan atare sukaji muryanshi hakan yasa itama granny tatashi da sauri itama sukai stairs suka sauka kasa daidai Imam yacire hannunshi dagakan kirjinta yakoma jikin kujera yazauna tareda dafe kanshi ahankali yana innalillahi wa inna ilaihi raji'un, chak Granny ta tsaya a stairs tana kallon Fatima that was lying there dead gabanta nafaduwa sosai saikuma ahankali takai hannunta kan glasses din idanunta tacire ta kalleta sanan tasake maida glasses din ta kalleta tace "Fadimatul Zara'u!!".

_Erotic Ideas group na matan aure zalla ne, group ne damuke program guda HUDU aduk sati, ranakun sune ALHAMIS, JUMMA'A ASABAR da LAHADI._

_Duk ranan Alhamis munayin program mai suna MARRIAGE LIFESTYLE, wato ZAMANTAKEWAN AURE, inda nakema mata lectures kan yanda ake zama da miji dakuma dabarun zama da miji, ranan jumma'a kuma muna program din damuke kirada TALK & HEAL

wato yi magana ka warke, inda matan aure zasu gayamana matsalolin dasuke fuskanta agidajen mazajen su, zasu iya turamin ta pc idan basuson asansu nisainai forwarding group mu taimaka musu da shawarwari dakuma dabarun dazasubi su magance wanan matsalolin, sai ranan asabar shine ranan LECTURES, inda zan dauki darasi dake dauke da dombin ilimi abu wanda ya dace mata su iya dangane da aurensu, mu koya musu ayi magana akai sosai, sai ranan Lahadi zamuyi lectures akan ilimin daya danganci yanda zaki gamsar da mijinki sanan ki gamsar da kanki, kisaka mijinki ihu agado yana kururuwa yana sambatu, mukoyar dake yanda zakiyi spicing up sexlife dinki, and yanda zaki dinga rayuwa da mijinki kullum kaman sababbin aure._

_Idan kinason shiga wanan group din zaki turo 2000 to 3107021073 aisha Muhammad first bank, saiki turo evidence of payment ta watsapp number na 07012181461 sainai adding naki a group din, wata daya ne group din, idan kinason ki cigaba da zama duk wata dubu dayane 1500 ne subscription, sababbin zuwa kUma new member zakiyi register is 2k ne, don karin bayani zaki iya tuntubata a number ta 07012181461_
M Shakur ❤

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

_MASIFAFFIYAR KAUNA_

✍🏾M SHAKUR

EPISODE 5️⃣3️⃣&5️⃣4️⃣

Granny takira sunan da karfi dayasa dukansu suka juyo suka kalleta kafin ahankali tabi ta gefen Ammi tasauko daga stairs din tazo inda Fatima take kwance akasa ta tsugunna tana kallonta yanda yarinyar tayi sanan tajuyoda kanta ta kalli Dr tace "Imamu a ina kasan yarinyar nan? A ina kasamo ta" motsin dataji Fatima tayi yasada sauri ta kalleta, Rayyana ce tace "Yaya tayi motsi" da sauri yazo wajen yasake maida stethoscope dinshi kunne yadura akan kirjinta jin

heart dinta na beating yasa ya lumshe ido tareda furta. "Alhamdulillahi Rabbil Alameen, she's back" yafadi ahankali duk suna kallon fuskanta yanda take kokarin bude idanuwanta, bude idanun tayi ahankali sanan tadaurasu akan dukansu yan dakin har lokacin komina jikinta yamata nauyi, da sauri Granny tashafa kanta tace "Zara kin ganeni? Baabar kice" shiru tayi tana kallon Baban wani irin, kallon Ammi shi yayi yace "Ammi please amata wanka da ruwan zafi ta chanza kayan nan awanke kan nan nata, sai kubata tea tasha zanje hospital na kwaso magani nazo namat treatment i will tell you everything" gyadamai kai kawai Ammi tayi tana kallon Fatima itama, dasauri Granny ganin yasake zamane yana kallonta tace "wuce katafi mana Imamu" tashi yayi ya kalli Ammi yace "Ammi car key" gaban TV stand tanunamai, key motarta yagani hakan yasa yadauka yawuce yafita daga gidan.

Shadaya saura ya shigo gidan da katon ledan magani, Babanshi yagani da Granny dakuma Ammin shi afalo hakan yasa yadan tsaya yana kallon mahaifin nashi. "Are you standing there kozakaje kasaka mata abinda yakamata" Baban yay magana hakan yasa yawuce sama, adakin Granny yaganta kan gado an mata wanka ansaka mata doguwan rigan atampa light mara nauyi na Rayyana tana kwance kan gado idanunta biyu sai kallo su Rahma take har lokacin batace musu uppan  ba, karasowa yayi yana kallonsu yace "tasha tea"? Rahma ce tace "kadan tasha bada yawaba amman" gyadamusu kai yayi ya shiga saka mata ruwa yay allurai a ruwan sanan yamata wani allura a vein ya tsaya chak yazuba hannu a aljihu yana kallonta kaman yanda yaga tana kallonshi da idanuwanta dake rufewa sanan idanun suka rufe tass bacci mai karfi ya kwasheshi yawuce ya sauka kasa kannenshi suka biyoshi, waje yasamu kusada Granny shi yazauna yace "when did you come back from UK Granny"? Murmushi tayi tashafa kanshi tace "nagaji da zama dasu wlh, ni nafison kasata Nigeria, abeg ciwo bata kisa sai in lokaci yayi nadai kwaso magungunana zanyi kwana biyu jibi zantafi Abuja gidan kanin Babanka achan zan zauna sabida consultant dina yahadani dawani abokinshi shima baturene dazai dinga dubani a anan Abujan" gyadamata kai yayi, sanan ahankali tace "muna jinka Imamu a ina kasamu diyata"? Dasauri yace "wai Granny itace Fatimar da idan nazo UK kike cemin kinyi kewa har kikasa naje wani gida anan kano dana dawo nadubo mikisu sabida you lost her father's contact akacemin sun tashi" gyadamaikai tayi tace "itace Fatima Zara diya ga Muhammad, a ina kasanta"? Nan yafara koromusu bayani right from ranan da aka kawota hospital dinsu tana rashin lpy yay admitting nasu har zuwa ranako irintayau. Sosai suka girgiza da Al'amarin, Abba yace "natausayama yarinyarnan wlh, Allah ne yaturaka exam dinan a lagos kawai sabida ka cetota amman cousil exam yawanci ma anfiyinshi a Abuja wanan karanne naga anyi a Lagos, am proud of you Son, shikuma Babanta! Hmm akwai Allah kawai" cikin fushi sosai Granny tace "wani irin akwai Allah Abubakar? First thing tomorrow in the morning tunda Allah yasa kasan gidan Imam zaka tukani nida ubanka ka kaimu gidan inaso naga Muhammad ido da ido ya maimaitamin abinda yafadin maka na gasgatar danni nasan yanda yaeson yarinyar nan tun tana yar karama, inyaso Maryam kesaiki zauna da ita anan gida" gyadamusu kai Ammi tayi tace "In sha Allah" nan suka cigaba da hirarrakin duniya daga baya Imam yatashi yahsiga yadubata har lokacin tana bacci sanan yawuce yasauko yamasu Dad saida safe yawuce yakoma flat dinshi.

WASHEGARI!!!
Karfe takwas Granny tashiga dannamai kira awaya, kiran wayan yasa yabude ido da kyar danyagaji yana dawowa daga sallan asubahi yakoma bacci, wayan yajawo yakara a kunnenshi ahankali yace "Granny" cikeda Masifa dan tanada fama sanan bata tolerating nonsense tace "kasandai kai nida father ka muke jirako" ijiye wayan yayi da sauri yasauka kasa sake dauro wani sabon wanka yayi yafito ya shirya cikin wata ash shadda bugagga yadauki hula yakafa aka yasanya takalmi yafito yana rikeda car key dinshi datun asubahi yacema gateman dinsu ya wankemai.

Flat dinsu ya shiga yaga daga Ammi sai Granny su awajen da alamun sun gaka break harsun watse, gaidasu yayi, Ammi tace "kajeka dubata ta tashi amman bata kula kowaba tea kadai tasha" gyadama Ammi kai yayi yazo zai mota ya shafa fuskar kakan tashi yace "Smile now Granny" hararanshi tayi takalli Ammi dake musu murmushi tace "danki yagama rainani wlh" cikeda wasa Ammi tace "ba'a shiga tsakaninku, keda jikokinki mu namu ido" hararan Ammi tayi tace "ai dama bamuce ku sakaba" dariya Ammi tayi tace "mezakici da dara" ahankali tace "fruits nakesha darana, da daddare kuma tuwon accha zakimin da miyan kubewa danya" gyadamata kai Ammi tayi.
Ahankali tabude dakin datake ciki yashiga babu kowa ita kadaine dansun tafi makaranta su Rayyana, idanunta biyu tana kallon hannunta kawai tai lamo kaman mara lafiya, karasawa bakin gadon yayi yazauna ahankali, saikuma yadauki stethoscope dinshi dake gefen gadon ya sanya sanan yadubata, tareda cire drip din yamakala mata wani har lokacin hannunta take kallo ko motsi batayi da ido yay allurai cikin ruwan sanan ya tsaya jim yana kallonta saikuma ahankali ya tsugunna ta yanda fuskanshi zai dinga ganin kwayan idanunta, murya chan kasa yace "Hey Fatima" saikuma yay shiru ganin batabar kallon hannunta datake kalloba hakan yasa yadaura hannunshi ahankali kan inda take kallo ahannunta, ahankali yace "nasan you can hear me perfectly fine dan yanzu fine, and u can see me, I want you to know that all of us here will support you, you have a full family anan yan uwanki yarenki dazasu taimaka miki, kin dawo daya daga cikinmu, Baabarki is here as well am sure kinganta, just take your time process all this emotions ki manta da duk wani abu dayasameki abaya ki daukeshi amatsayin kaddara sanan kigodema Allah and move on kema kifara makaranta kaman su Rayyana and Rahma, you are free now Fatima u can do anything you want, you have your life, so own it kitashi and be free you have three sisters already anan and let go off the past, now dayakamata kina farinciki karki bari emotions yarikeki na past dinki okay" yay maganan yana kallonta har lokacin tana nan yanda take batare datai motsi ba, gently yajanye hannunshi dagakan hannun nata yajuya yafita ahankali tareda rufomata kofa.

Afalo yasami Granny da Abban shi Ammi na kitchen dayar aikinsu yace "mutafi" gaba yayi suka

biyoshi abaya suka shiga mota yajasu har zuwa unguwan su Baba, har kofar gidansu sukai parking dukansu su ukun suka iso, daidai lokacin wani yaro yafita daga gidan da sauri Granny ta tareshi tace "kai jekace ana sallama da Malam Muhammad" da sauri yaron yace "Baban su Habib"? Gyadamai kai Dr Imam yayi yaron yajuya da gudu yay cikin gidan, ba'a wani dauki lokaci ba saiga Baba yafito yaci gayu abinshi yay kyau kaman bashiba yana sanye da jallabiya fara mai kyau yar kanti, ganin Granny yasa yabude idanu cikeda mamaki yakaraso wajen yace "Hajiya, marhaban dasu lale" murmushi sosai Granny tamai tace "Malam Muhammad daman rai kan ga rai" dasauri yace "aikona kiraki baya shiga" anatse tace "wani ciwo nayi da aka hanani amfani da waya kwata kwata" "assha Allah sawake" yay maganan yana bama Abba hannu yana kallon Dr Imam irin kallon bana gayamaka karka kara zuwa gidana ba, ganin kallon yasa tace "jikana kenan Imamu, ga mahaifinshi nan" tanuna Babanshi tace "dashi da kanninshi na Abuja saikuma yata dake UK ne Allah kadai yabani aduniya, wanan ma a Abuja suke ai katuna lokacin yanda nake yawan zuwa Abuja basu wani dade da dawowa kano ba, asibiti babanshi yabude anan, idan kuma ina Abuja ina gidan kanninshi ne kasan anhanani zama ni kadai sabida ciwo" gyadamata kai Baba yayi saikuma ya murmusa yace "bismillanku ai bana barku anan tsaye ba" yay cikin gidan suna biyedashi har zuwa falonsu da babu kowa gashinan agyare kaman yasani yanzun nan yagama gyarawa dan ya tsani datti yara kuma duk sun tafi aiki banda Abida dake bacci da mamanta adaki, Granny ne tabishi tashiga falon Abba da Imam suka tsaya kasancewansu maza dole sai anbasu izinin shiga ai zasu shiga, da sauri Baba yadaga labulen yace "ku shigo dan Allah" sallama Abba yayi yashiga tareda Imam suka sami waje suka zazzauna shikuma Baba yashiga ciki da sauri yadan daddaki Mama dake bacci tana sanye da doguwan riga yace "tashi Ruka munyi manyan baki" da sauri tanude idanunta ta kalleshi, murmushi yamata yadauki hijabi yabata yace "Hajiya ce data taba bani achaba nai aiki aikin ganeta lokacin damuna amarya dani dake da Fateema muna zuwa wajenta" daure fuska tamau tayi tace "Baabar Fatima" da sauri yace "eh" kwafa tayi tanunashi da yatsa tace "saura inga anmaka maganab Fatima kafadi abinda bai kamata ba" daure fuska yayi yace "nace kidenamin maganan yarinyae nan" murmushi tayi tareda sauke ijiyan zuciya ranta fess ta karbi hijabi tasaka sanan ta sauka dagakan gadon, suka fito falon Mama tana kwasan pure water a hannu cikeda kunya kaman na gaske Mama tace "wanake gani haka Baabar Faty ido kanga rai dama" murmushi Mama tamata tace "Rukkaya" anatse tace "naam ina wuni ina gajiya" sanan ta gaida su Abba tace ga ruwa kusha duk sukace sun koshi sun gode akai shiru, sanan anatse Granny tace "Malam Muhammadu wata maganace muhummiya takawoni wajenka" anatse ya gyara zama yace "too too ina jinki Hajiya" gyara zama glass din kan idanunta tayi dake karamata karfin gani sanan ta kalli Baba takoromai bayani tundaga farko har karshe wanda Imam yafadi mata sanan tanisa tace "dudda abinda su mutanen lagos suka bama Imamu labari kace bakason yarinyar, da still yanda kafadima Imamu shima dayazo nemanta saisa nima natako takanas takano dannazo naji da kunnena dan yanzu ahak yarka na gidanmu babu lpy, kuma ayanzu babu abinda yarta ke bukata irinku iyayenta after wahalan rayuwa datasha ayan watannin nan na kimanin watanni shidda dabata gida koba hakaba" tunda tafara magana take kallon Baba ganin yanda ranshi kenan abace yay kini kini darai daga fara ambaton sunan Fatima datayi harta gama, kasa magana yayi Granny tace "kayi shiru" cikeda rage murya trying to suppress his anger yace "Hajiya mun dade muna tare kuma kinsan inajin magananki, amman kinga wanan yarinyar dakike magana nifa ba y'ata bace, kawai nagayamiki y'ata ce

sabida nina tsinceta da bomb yatashi agarinmu naganta tana walagigi akan titi, amman nidai ba y'ata bace" da sauri Granny tace "mekake cewa hakane? Idan bakaine ubanta ba waye uban nata Malam Muhammadu? Kamannin dakukayi da itafa"? Cikin dan fushi yace "kama ai ta Allah ce, nataimaka mata nabata abinci nabata sutura tun tana yar tatsitsiya aikam zata iya kamadani, ni Wlh Hajiya ko kadan banson inji kina ambaton sunan yarinyar nan jinake raina yana baci matuka, ni Fatima ba y'ata bace aikoshi wanan yaron" yanuna Dr Imam, "dayazo neman aurenta cemai nayi niba ubanta bane yaje chan yanemo ubanta yabashi aurenta babu ruwana alamarin yarinyarnan bansan komi nataba, bankuma son komi nata" yanda yake hargowa kaman ba salihin mutumin datasani kwanakin bayaba dako magana bayayi mai kunya yasa itama ta tsinke dama Allah yahore mata iya fada, tace "dubanni nan da kyau Muhammadu, kabar ganina da karamin jiki ko d'ana nabiyu kanin wanan....." tanuna Abban su Dr Imam, tace "koshi ya girmeka, ahaihuwa nayi kaman ka, biyu dan bakada wani babba anan dazai tsawatar maka toni na isa, ka saurareni nan dakyau, koda wasa karka sake furta abinda kake fadi, yarka ba yar iska bace, bayar shaye shaye bace ballema ace wani mugun hali takedashi yasa ka tsaneta, a'a, salihar yarinya, baiwan Allah ga dumbin ilimi both na addini da islama ne kakema haka kana cewa ba yarka bace, watakeda shi? Bakuda kowa anan garin, kauyenku gabaki dayama ya bombe kowa yamutu sanan kace zaka wulakanta yarinya, kamaida y'a namiji sabida karufama kanka asiri bayan kasan koyin da Ma'aiki rasulu yahana haramun ne abinda kayi, yanzu kuma an samu an ceto yarinya kuma kace bazaka karbeta ba itaba yarka bace, kaza kaza kaza, wlh kaji tsoron Allah, hakkin marainiyan Allah nan bazai barka bacci ba" tashi Baba yayi idanunshi sunyi jazur yace "hajiya tundadai nabaku girmanki baki bani nawaba kitashi kibarmin gida" dasauri kowa na falon ya kallai, Abba zaiyi magana Granny tadagamai hannu tace "karka sake kasa baki anan barni da fitsararren yaron nan" tajuya ta kalli Baba tace "baza'a fitaba ka daukeni ka fitar dani nace Muhammadu inka isa, kadaukeni kafitar dani inka isa kaji" tai maganan tana kumfan baki itama, baba dayaga tafishi iya hauka saiya koma yazauna tace "kuma anjiman nan zanzo dakaina nadawo maka da yarka, ta zauna akarkashinka" wani kallo yama Mama yace "Hajiya barganin kin taimaki rayuwata, ko Allah ma yasan I appreciate duk abinda kikamin saidai wanan ba huruminki bane, kuma wlh wlh wlh kinda kindaiji rantsuwata sau uku ko, na rantse miki da girman Allah duk randa kokuma ince duk randa yarinyar nan zata taka kafa gidan nan saina koreta saikuma namata illa, Fatima ba y'ata bace, bansonta, bankuma kaunar ganinta har abada, yarinyar nan is nothing but a bad luck, ta lalata rayuwana yanzu da bata rayuwa tamin siga ina aiki, dan haka karki tunanin kawota ma dan wlh ko kafa bazata saka adakin nanba, nafada nakara niba ubanta bane, niba ubanta bane, niba ubanta bane,  duk yanda zakuyi da ita kuyi ai bance kowa ya riketa ba, itama yarinyar nafadi mata niba ubanta bane, harnabar duniya banson kara ganin Fatima arayuwata, tajechan duniya tayi duk yanda tagadama da ita, ta tagaiyara, ta kaskance ta wulakance niduk ba damuwata bane yarana biyar maza hudu mace daya wacce take abida su kadai garen" yafada rai abace dayasa jikin Granny sanyi, takai hannu tashare hawayen daya zubomata tasake kallonshi tace "to kasha kuruminka indai inada rai, sanan indai yaran nan nawa na nan, kagansu nan da Muhammad, da Iburahima na Abuja dakuma Aishata ta UK inhar suna raye kodani bana raye wahalan Fatima yazo karshe namaka alkawarin nan, xamu maida Fatima mutum, Fatima zata koma zatai makaranta, zata zama wani abu zakazo zaka cije yatsa sanan zakai dana sani, kadaice Fatima ba yarka bace ko"? Dasauri Baba yace "nafadi nasake, zankuma kara yanzu,

Fatima Zara'u ba y'ata bace, karkuma tasake amfani da sunana as surname dinta, niba ubanta bane ehe" murmushi irin mai ciwon nan tayi tace "shikenan, Alhamdulillah natako da kafata nazo naji da kunnena, lawyer na zaizo harnan gidanka yanzun nan yabaka paper kai signing cewa kaiba ubanta bane, dagayau nine uban Fatima, custody dinta yadawo wajena, rayuwace zaka gani Malam Muhammadu" tamike tsaye azuciye ta kalli su Abba da jikinsu yay sanyi tace "kumutashi mutafi" tashi duk sukayi, Granny ta kalli Mama datai dariya tace "ke y'a mace ce, kuma kituna d'a nakowa ne, thank God kinhaifa" dasauri Mama tatashi tace "ahhhh nanfa daya tunda kuka fara abunku kinji nasaka muku baki? Nime ruwana dakike neman yima yarana baki ba gaira ba dalili hajiya haduwan kan titi" dasauri Imam da tuntuni Baba kehanashi magana yace "Granny let's go pls" tabe baki Mama tayi tace "yoo kuyi zancen ku chan ni bani aciki, uba yace ba yarshi bace mekikeso nayi? Yarana ma kadai sun isheni balle nakara da wata daba yar mijina ba" Granny zata kara magana Abba yakamata yawuce yafita da ita Imam yamare musu baya, suka bude bayan mota suka sakata Granny tafashe da kuka sosai,  Abba yahsiga baya yana lallashinta, Dr Imam kuma yakoma gaba yaja motar.

Cikin kuka Granny tace "what a cruel world we live? How can a father abandon his 19yr old daughter haka da yanzu tana tender age idan ba'a kulada tarbiyanta ba anything can happen eh? Wanan wani irin abune, giyan wake yasha ne komene, wlh xan nunamai waye ne, har abada bayi kara ganin yarinyar nan, Muhammadu kiramin lawyer mu kabashi sako yaje gidan" babu musu Abba yakira lawyer danshima ranshi abace yake yabashi sakon saida yagama tass sanan tashare hawayenta tace "Muhammadu da yarinyar nan zan koma Abuja tai zamanta dani awajen nasaman mata University tafarayi" faduwa sosai gaban Imam yayi, Granny tacigaba tace "banmaso ta cigaba da zama agarin nan ballema taji tanason zuwa ganin ubanta, zaisha mamaki wlh" gyadamata kai Abba yayi yace "hakan nada kyau, zan kira Ibrahim muyi maganan" babu wanda yakara cewa komi a motan buni buni tana share hawayen datakasa denayi tsabagen tausayin Fatima har sukakai gida.

_Erotic Ideas group na matan aure zalla ne, group ne damuke program guda HUDU aduk sati, ranakun sune ALHAMIS, JUMMA'A ASABAR da LAHADI._

_Duk ranan Alhamis munayin program mai suna MARRIAGE LIFESTYLE, wato ZAMANTAKEWAN AURE, inda nakema mata lectures kan yanda ake zama da miji dakuma dabarun zama da miji, ranan jumma'a kuma muna program din damuke kirada TALK & HEAL wato yi magana ka warke, inda matan aure zasu gayamana matsalolin dasuke fuskanta agidajen mazajen su, zasu iya turamin ta pc idan basuson asansu nisainai forwarding group mu taimaka musu da shawarwari dakuma dabarun dazasubi su magance wanan matsalolin, sai ranan asabar shine ranan LECTURES, inda zan dauki darasi dake dauke da dombin ilimi abu wanda ya dace mata su iya dangane da aurensu, mu koya musu ayi magana akai sosai, sai ranan Lahadi zamuyi lectures akan ilimin daya danganci yanda zaki gamsar da mijinki sanan ki gamsar da kanki, kisaka mijinki ihu agado yana kururuwa yana sambatu, mukoyar dake yanda zakiyi spicing up sexlife dinki, and yanda zaki dinga rayuwa da mijinki kullum kaman sababbin aure._

_Idan kinason shiga wanan group din zaki turo 2000 to 3107021073 aisha Muhammad first bank, saiki turo evidence of payment ta watsapp number na 07012181461 sainai adding naki a group din, wata daya ne group din, idan kinason ki cigaba da zama duk wata dubu dayane 1500 ne subscription, sababbin zuwa kuma new member zakiyi register is 2k ne, don karin bayani zaki iya tuntubata a nUmber ta 07012181461_
M Shakur ❤️

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

✍🏾M SHAKUR

EPISODE 5️⃣5️⃣&5️⃣6️⃣

Parking yayi Abba shiya fara futowa yabudema Granny dake kuka har lokacin kofa yace "Hajiya dan Allah kiyakuri kidena kuka kinga bawani lafiya ce ta isheki ba" yay maganan yana fitoda ita daga mota sukai cikin gida, Ammi dake kokarin saita dinning ne ta tsaya chak ganin an shigo da Granny tana kuka dasauri ta taho takalli Abba tace "Hubby maiya sami Mama kuma take kuka"? Kafin Abba yabada amsa cikin kuka sosai Granny tace "barni kawai yau naga abinda tsawon rayuwata ban taba ganiba, tayaya zaka wulakanta yar karaman yarka? Meta maka? Wani laifi tamaka? Tanada wani mummunan haline? Ka wulakanta yarinya kamaida yarinya namiji, ta wahala, jibi yanda sauro dawata tsiyace duksun cinyeta amman mutumin nan ko'ajikinshi wai bayarshi bace idan mukama kawota saiya nakasata sanan yakorata, duniya ina zaki damu? Talauci nataba ma mutum kwakwalwane wai? Wlh wanan abun yay min ciwo sosai kinji Maman su Imamu, yarinyarnan tabani tausayi matuka" takara fashewa da kuka, bude kofa Imam yayi yashigo kaman ance yadaga kanshi ya shigo Fatima yagani aduke ta tsugunna akan stairs dinsu tadaura kanta akan cinyarta ga cup din tea agefe yasa yamaida kofar yarufe yay stairs da sauri hakan yasa duk suka kalli stairs din, ganinta yasa Granny tasake rushewa da kuka tayi stairs din itama daidai yakai gabanta tsugunnawa yayi ahankali agabanta yakira sunanta. "Fatima" dasauri Ammi data biyo bayan Granny tace "naga ruwan daka samata yakare nacire nasagale, nace metake sha'awaan ci tacemn tea, shine nabata nace bari nazo kitchen ina girki ne, halan tagaji da kwanciya ne tafito" ahankali Granny takai hannunta tadago kanta dagakan kafarta tace "Fatima" dagota sukayi sukaga fuskarta ko kadan babu hawaye ammam the kind emotions dakuma yanayi dake cikinshi zai iya saka kafashe da kuka, gyara zama Granny tayi tazauna kan stairs din sanan takai hannayenta biyu ta tallabo fuskar Fatima tace "Faty Zara na, nasan duk abinda muke cewa kinji amman inaso kisani mudin nan saimunfi miki iyayenki, tun kina karama naroki mahaifinki yabani ke yaki da dake zan tafi UK abina, ki dauki wanan rayuwan da wahalan dakikasha abaya as kaddara, ki manta dakomi ki manta da kowa na daki ada, saisama zan bar kanon dake Abuja zamu koma kifara karatu kinji, I will be your father and your Mother kinji, I gotcha Zara" sai alokacin tadaga idanunta takalli Granny ashanye sabida kalman datafadi na karshe wanda prince ne kadai yatab fadamata wanan kalman, hawaye taji yazubo mata dasauri takai hannu zata goge hawayen Granny tarike hannunta tace "no no no, yi kuka Zara, ki fitarda duka abinda ke ranki ayau dinan dam daga gobe sabuwar rayuwace, cry kinji kin cutu sosai" kaman jira take tawani irin fashe da kuka sosai tafad jikin Granny ta kankameta tace "Baaaabaaaaaaa, Baaaba nagaji dakomi kaman na mutu nahuta kawai nakeji" da sauri Ammi tajuya jin hawaye yazomata Baba kawai ya girgiza kai yabi Ammi zuwa kitchen din dayaga tashiga dan yasan kuka zataje tayi dan kowa yaji rayuwan da Fatima tayi dakuma abinda mahaifinta yamata xaisa kaji kana tausayin yarinyar, tayi kuka iya kuka sanan Granny tasamu tai shiru, tagoge mata hawayen tass tace "no more cry" sanan takalli Dr Imam dake gefenta yace "kadauki ATM card ajakana kaje kasamo mata cream dazaisa wanan kurajen da cizon sauran kona menene ma dake jikinta yabace pls" sanan ta kalli Fatima tace "muje kiyi wanka" tadagata sua wuce ciki yabisu da kallo kafin ahankali yatashi yawuce yafita.

Haka ranan tawuni babu wani zazzabi kodaya ajikinta kawaidai kana ganinta kasan she is not happy, batada magana su Rahma sun shigo sun jajjatada hira amman shiru, Granny ne kawai

kesata tai magan tayi ko Dr Imam batamai magana sai ido, abinci ma taci ba laifi, gabaki dayansu sunawani irin jida ita kaman sun sami kwai.
Da daddare Lawyer Abba yazo yakawomai documents din da Baba yay signing kan ba yarshi bace sanan yakawomao credentials din yarinyar dayasa lawyer ya amsa wajen Baba dan dasu Ibrahima zai nema mata makaranta.

WASHEGARI!!
Tunda sassafe aka fara musu girke girke ana loda kayan Granny a mota dan da motan gida za'a kaisu sudai suna kasa yaran na sama wai acewansu zasu taya new kawarsu Fatima shiryawa.

Dudda yadda take bai hanata tai mugun kyau ba, wata doguwar bakan riga sabuwa Ammi takawo mata datajw Umra tasayo, sanan suka sakamata kwalli a ido dan idanunta sun kore dayawa, saikuma suka samata ban baki akan lips dnta daya bushe sosai sai abin yayi kaman tashafa jan baki, murmushi Rayyana tayi tace "kinga yanda kikai kyau kuwa, banson ina zuwa hutu gidan Baffa sabida yacika fada amman yanzu sabida je zan dinga zuwa I promise" gyadamata kai Fatima tayi, Rahma tace "kunji Granny na kwala mana kira muje" ahankali ta tashi dagakan kujeran tayi kyau sosai Rahma tabude kofa Ya Imam suka gani agaban dakin, yau yana sanye da kananan kaya, farin riga dakuma jean dogo baki idanunshi sanyeda fararen glass ganinshi yasa da sauri kannen nashi suka wuce itakuma takasa tafiya ta tsaya chak kanta akasa tana wasada yatsunta, ahankali yashigo dakin yamaida kofan yarufe tareda jingina da kofan yay folding hands dinshi akirji sanan murya chan kasa yace "Fatima" kasa amsawa tayi hakama takasa dagokai ta kalleshi, fuzarda iska yayi ahankali yace "take care of yourself idan kinje Abuja, be serious with school, I will try na karbi transfer zuwa Abujan idan ban samuba zan dinga zuwa weekend, forget everything about your past and move on kinji" gyadamai kai tayi ahankali batare data kalleshi ba, dan jim yayi sanan yatako ahankali yazo gabanta ya tsaya still kasa dagokanta tayi but you could see yanda gabanta kefaduwa, hannunta yakama ahankali sanan yasaka mata ledan sabuwan wayan da yanzun nan dawowanshi kenan daga zuwa siyomata yace "be using this phone, u will need it idan kika fara school sabida assignment and the rest, Allah kiyaye hanya" yana maganan yajuya yafice daga dakin dasauri.

Tadade tsaye awajen kafin ahankali takalli ledan wayan hannunta, ita kanta batajin dadin kanta she just loose interest in anything and everything, jin Granny ta kwalamata kira yas tabude kofan ahankali tafito ta shiga saukowa kasa Granny na kallonta tace "Ammin su Imamu zokiga yar wajena yanda tai kyau" dariya Ammi tayi tace "ahhh lallai tawajenki kam tahadu wlh" shide Abba dake zaune afalo murmushi take, da sauri Rahma tace "Granny kinga ninefa na shiryata" dasauri Rayyana tace "its a lie, nine wlh Granny" duk dariya akayi saida tazo wajen Granny sanan tace "gani Baaba" murmushi tamata tace "jekima Abba da Ammi sallama" har wajen kujeran da Abba kekai Mama nazubamai ruwan lip tea akai taje, ta tsugunna har kasa tace "Abba zamu tafi, Ammi, nagode sosai Allah yasaka da alkhairi" kanta Abba yashafa yace "Allah yamiki albarka Fatima Zara" Ammi tace "Allah yakiyaye hanya daughter zamu dinga waya kinji,

tashi abinki" tashi tayi ahankali Granny na murmushi tace "to saduwan alheri" rungumeta su Rahma sukayi tabasu kudi sosai sanan duk aka rakosu har mota, shiga motan sukayi, Granny tace "tundashi miskilin vazai iya fitowa yamin addu'a ba acemai natafi" duk dariya akayi Ammi tace "hospital fa yacemiki xai tafi dazun nan daya sakko kasa" dan ware ido tayi tace hakane fa sanan suka shiga musu bye su Rahma na suna hutu zasu taho Abujan, har suka fit daga gidan.

Sundanyi nisa sanan tadauki ledan wayan tabama Granny ahankali tace "Baaba Ya Imam yabani" dasauri takarba tace "masha Allah menene aledan" tai maganan tana cirowa daga kwalin Samsung wayace mai kyau A72 sabuwa gal, murmushi Granny tayi tana bata back tace "iyye Yaya Imamu yasaima y'ata waya, to akashe lafia enjoy your phone,  bansan ko kadan ina ganin damuwa kan fuskarki kinji" tai maganan tana kamo kanta tareda daurawa kan cinyanta tace "kwanta" kwanciya tayi ahankali, Granny tashiga shafa kanta tace "zan rikeki amana Fatima, nine mamanki nine babanki, banson komi kina boyemin kome kikeso komeyake damunki kidinga fadamin, I mean komenene kinji, banson ina ganinki so sad, kinga inda zamu gidan Ibrahima ne matarshi nada kirki sosai kuma tanama fita aikin ta, shi datake rikakken dan bokone yara biyu kacal ya haifa, first yaronshi is just 15yrs old yanama boarding house, SS2 yake, sai yarshi tabiyu tanada 7yrs Amna ita kuma tana primary six ta iya surutu, so you will not have any problem with them, idan mukaje ma bakison gidan inada my own personal house dina saimu koma, dama Doctors ne suka hana ina zama nikadai sabida ciwukana, ga diabetes, ga hawan jini, gakuma asma, saisa nake zama da yarana but yanzu ma naji sauki sosai Dr's din UK na sun iya aiki I hardly have attack yanzu, so I want you to be happy, idan kina murna nima I will be fine hankalina ya kwanta nasan cewa ban tauyeki dakomiba, muna kaiwa zankira telana adinko miki kayayyaki kala kala, zamu fita shopping, muje dunes kisai jakunkuna da takalma da gyaluluwa sabida ki shirya fara school kema ki shiga cikin yaran manya ki more yanmatakan ki kaman kowace yarinya of your age kinji" gyadama Granny kai tayi ahankali, fuskanta Granny tashafa tace "to yimin murmushi mana Zara na" batason matan tadamu hakan yasa tamata murmushi bako karamin Dady Granny tajiba haka tadinga mata hira har bacci ya kwasheta Granny na shafa kanta tana kallon fatarta tace "suna isa kaduna zata mata order su scrub glow oil dasauran kayayyakin Glow & Go naturals, sabida hasken fatarnan nata dayadan dishi yafito tadawo da kyanta gashinta zatakaita saloon gobe awanke ayaryada mata kitso, zata gyara yarinyar nan this is just her promise zata zuba kudi ajikin yarinyar  nan zasuga yanda yarinyar nan zata dawo, saima tafara makaranta tafara ganin yanda sa'onninta ke gayu sosai zata kara kilewa ne.

Saida suka shiga Abuja sanan Granny ta tadata tace "tashi ki kalli Abuja" tashi tayi tajuya tana kallon waje ta glass harsukakai wani anguwa locust agaban wani dankareren gida dayamafi nasu Imamu girma taga sunyi horn, aduka yaranta Baban su Imam Dr nema wanda baida kudi sosai dudda yanama mallakin private asibitin kanshi, gateman taga yafito yana ganin Granny yakoma ciki dagudu yabude kofa suka shiga cikin katafaren gidan, daidai anbude kofan flat wata cute yarinya fara sol tafito tana sanye da short gown nayara, hannunta rike da sweet mai tsinke tanasha tana hango Granny tabuga uban ihu. "Mummy Granny is here" sanan tataho da gudu tana tsalle. "Oyoyo Granny, oyoyo grandma" daidai lokacin Granny tafito tabude mata

hannu aiko yarinyar tadaka tsalle sai jikinta ta kankameta tace "Granny am happy u are back, what did you bring for me" tai maganan tana kallon Zara data fito daga mota, murmushi Granny tayi tace "many things, ya akayi aka miki tsifa rabi akabar rabi"? Kaman zatai kuka tace "Granny tsifan Mummy zafi naki wlh babu" dariya Granny tayi tace "to gobe zan miki saina bada dukanku dakeda Anty Zara akaiku saloon" dasauri yarinyar tace "who is Anty Zara Granny" nunamata Zara dake gefenta tayi tace "ga Anty Zara nan" ware manyan idanunta tayi tana kallon Zara data kakalo murmushi tasakinma yarinyar tace "Granny is she from the Arabs irin na makka damuka je? She looks like them,  is she from there"? Dan dariya Granny tayi tace "no she's not from there she's from Maiduguri" baki tabude zata sake magana sukaji murya. "Can you please allow my mother to rest and go to your own mother" yanuna kyakkyawan matar dake kusada shi da akalla zatai 38 ko 39 tana sanye da hadaddiyar atampa tana murmushi, dariya duka akayi banda ita data turo baki tasaki Granny ahankali takama hannun Zara tarike tace "then I will go to my Anty Zara" zuwa mutumin dazaiyi 57 yayi ahankali ya rungume Granny, ahankali yace "welcome home sweet Mum" itama matarshi har kasa taduga tace "barka da zuwa Hajiya, munyi kewanki sosai wlh" dagota Granny tayi tace "how are you Mariya" ahankali tace "fine" kana ganin yanda suke kaga educated couple, har kasa Zara ta tsugunna tace "ina yininku" da sauri Maman Amna tadagota tace "you must be Zara right" gyadamata kai Zara tayi ahankali, fuskarta tashafa tace "welcome, feel at home kinji, take me as your Mum and Dady as your Father" tanuna Baban Amna, sanan tace "let's all go inside and eat, Hajiya namiki fankasau na alkama da miyan taushe" shiga flat din sukayi, yahadu iya haduwa gawani hadadden kamshin turare dake tashi daga dakin, duk sukai dinning while mai gadi na kwasan kayan Granny zuwa side dinta, zama sukayi mijinta tafara zubama abinci sanan tazubama Kaka finkasau din data mata, ta kalli Zara tace "Zara mezakici ke" akunyace kanta akasa tace "anything Mum" murmushi daga Granny har danta Ibrahima sukayi, ita kanta saida Maman Amnan taji wani bala'in dadi yanda takirata tace "alright daughter bari nazuba miki abinda zanci ba boring abincin Granny ba" dariya duk sukayi Granny tace "oho dai" ta kalli Amna daketa kallon Zara da kanta ke kasa tace "kekuma lafiya kiketa kallon diyata" murmushi yarinyar tayi tace "Granny wlh I like her, this Anty Zara" duk dariya akayi Zara tadago kai ta kalli yarinyarnan hakanan taji tanason yarinyar kodan batada kanwa mace data girma hakane oho,  da hannu tamata alamu tazo hakan yasa ta taso dagudu tabar kujeran datake kusada Mumy ta tazo wajen Zara tazauna hannunta Zara takama tarike tana kallonta batare datace komiba, Amna tace "Granny maisa bata magana wai" Granny dahar tafaracin abincinta tace "kinga haka take Amna, ni aikinma dazan baki kenan kidinga koya mata surutu dan Allah" daidai nan Mumy tamikoma Zara abinci a plate, hadaddn jollof rice da salad ne agefe sai pepper chicken, karban abincin tayi anatse sanan tace "nagode Mum Allah ampana" hakanan gabaki dayansu saida ransu ya sosu da yanda tai godiyan tabasu tausayi saidai suka daure babu wanda yanuna mata, Mum ta kalli Amna tace "small Madam keme zakici" turobaki tayi ashagwabe tace "nina Anty Zara zamuci tareko" gyadamata kai tayi tadauki spoon dinta tabata sanan ita tadauki wani duk akai shiru aka faracin abincin, dudda batada apatite but surutun Amna da yanda taketa wasa tana raba musu abincin yasa suka cinye tass, Dady ne yafara tashi yatafi falo, Granny ma tawuce yarage Mum ce kawai dasu a dinning din tashi tayi ahankali ta kalli Amna dake kallonta, adan hankali batare dakowa yajiba tace "where's kitchen Amna"? Kofar kitchen dinsu Amna tanuna mata hakan yasa ta shiga tattare plates din dasauri Mum tace "mekikeyi daughter" ahankali tace "zan kai

kitchen ne" baki Mum tabude zata hanata Granny tace "Mariya ba'a hana d'a aiki, Zara ba bakuwa bace tazama yar gida" murmushi kawai Mum tayi batasake cewa komiba, Zara ta tattare plates din zata kwasa Amna tamika mata hannu tace "nima Anty Zara" guda daya tabata sanan suka wuce kitchen suka ijiye kafin sukara dawowa lokacin Mum tagama ta sake hade plate din tawuce dasu, Mum kuma tawuce falo, sanan tasake dawowa itada Amna ta gyara dinning din tass kaman ba'aci abinci akaiba sanan tawuce kitchen Amna nabinta kaman bindi tashiga wanke wanke......

Jin karan tana wanke wanke yasa Mum ta kalli Granny tace "Hajiya kinga wanke wanke take akwai mai aiki fa" murmushi Granny tayi tace "ki barta, aikin nan datakeyi zaisa ta watsake" gyara zama Dady yayi yace "ina credentials din nata"? Jakanta dake kan kujeran datake ta dauka tacirosu a file, sanan ta bashi ya karba yana dubawa, yace "yes tanada waec dinta tsaf duk taci science courses din, saidai batai jamb ba" anatse Granny tace "ai akwai schools din dazata iya farawa kafin next year yazo tayi jamb intaci saita fara University, inason nai keeping nata busy ne" gyadamata kai yayi yace "akwai friend dina dake running Private Health School, though anriga anyi admission, zan bashi inyaso saiya bata any course taje tafara, but dole a hostel zata zaune" dasauri Granny tace "a hostel"? Gyadamata kai yayi yace "eh, most health schools lectures dinsu suna farashi very early everyday,  sanan suna karatu harda na hauka, kinga kuma wanan dasun fara lectures definitely ana bata admission dole tazauna tai karatu sosai dan an wuceta, kibarta tazauna a hostel din babu abinda zai sameta babban school ne sosai achan karshen Abuja yake, inyaso duk Friday zamu dinga tura direba yana daukota tai weekend agida, ranan Monday da sassafe takoma" kallon Mum Granny tayi tace "ke Mamarta to kin yarda da shawaran mijinki"? Murmushi sosai tayi jin karan da Granny tamata tace "eh na yarda duk weekend zata dingayi agida Hajiya, kinga yanzu idan taje tana xama a hostel cikin student zata waye ta kile, sanan tadage da karatu duk wanan kunya da kas kallon mutane zata dena, idan yaso 1week din dayace mubashi zamuyi amfani dashi mu mata siyayyan school dakuma dinkuna ko Kaka, ni akwai ma wasu atampopina dazan bata" sanan tajuya ta kalli mijin tace "Dady zaka bamu kudi muje muyi shopping ko" gyadamata kai yayi yace "gobe tunda Saturday ne ba work saiku je dukanku" murmushi duk sukayi Granny tace "Allah yamuku albarka, shikuma lukuti na yaushe zasuyi hutu yadawo gida"? Dariya duk sukayi Mum tace "just last week yakoma sunyi resuming first term, shida dawowa gida ba yanzu ba saidai mujemai visit, Granny yasu Dr mara kiran mutane" dariya tayi tace "wanan ai kinga halin mijinki yadauko dan haka karma kiga laifin jikana ehe" dariya duk sukayi daidai Zara tafito rikeda hannun Amna, Mum tace "sannunku to da aikin daban sakaku ba" sauke kanta tayi Granny ta tashi tace "bari muje muyi wanka muyi salla, muje Zara" bin Granny sukayi suka wuce suka fita Mum tabi Zara da kallo, sanan ta kalli mijinta bayan nan tace "Dady wlh na tausayama yarinyar nan sosai at her age dai taga rayuwa" murmushi kawai yayi yace "such is life kowada kaddaran shi, dazaran tafara school tasaki jiki zata manta dakomi and move on" gyadamai kai Tayi tace "hakane" sanan suka cigaba da hiransu.

Bangaren Granny shima hadadde ne agidan, amman shi ba duplex bane sabida rashin lafiyanta

bata cikason hawa bene ba, but hadadden flat ne nagaske, ga durmemen TV afalon da speaker, ga kitchen ga dinning,  saikuma wani corridor, da dakuna uku keciki, daya daga cikin kofar dakunan tabude, hadadden dakine ga gado da aka gyara royal bed, ga sip din bango, ga bayi ga ac ta kalli Fatima tace "wanan shine dakin ki, kinaso ko kinason achanza miki wani abu"? Dasauri ta girgixa kai tace "inaso, Allah saka da alkhairi Baaba" bayanta Granny ta shafa tace "kidinga kirana da Granny kinji,  yanzu shiga ciki kije kiyi wanka akwai komi abayi kihuta, kekuma kibarta tahuta" tai maganan tana kallon Amna dake rikeda hannunta, raurau da ido tayi zatai kuka da sauri Zara cikin sanyin muryanta tace "dan Allah kibarmin ita Granny" murmushi Granny tayi tana kallon Amna dahar lokacin shirin kuka take tace "shikenan to" hakan yasa tafashe da dariya tanajin dadi, Granny tace "toku shiga" shiga sukayi suka maida kofan suka rufe itakuma Granny tasauke ijiyan zuciya tawuce tashiga nata dakin.

Haka ranan tawuni ko kadan Amna bata barta tahuta ba, surutu surutu, bata barta tai tunani ba, ta makala wayanta a chaji tanata kallon wayan har cikin ranta taji dadin wayan dan bata taba wayaba sai wanan, bayan Magrib suka wuce suka tafi flat dinsu sukaci abincin dare as usual tasake gyara dinning tawanke kwanukan dasukaci abinci dashi sanan Amna tajata sama zuwa dakinta tadinga mata surutu, sai wajajen 10 sanan Granny tamike ta kwala ma Zara kira, saukowa sukayi still Amna namakale da ita, ta kalli Mamanta tace "Mum ni i will sleep in grandma's place" tabe baki Mum tayi tace "agais dakansu zasu kadoki parrot" binsu tayi suka wuce side dinsu duk suka shiga Granny ta kulle kofan falo takashe wuta sukai balcony sanan tabisu har dakin Fatima tace "makesure kinyi wanka sanan kiyi nafila saiki kwanta kinji Zara, gobe zamu sayo harda kayan bacci" gyadama Granny kai tayi, sanan Granny ta kalli Amna tace "tsabagen azarbabi bamaki riko pajamas dinki ba" bari nakira Babanki yakawo miki" Kaka tai maganan tana fita zuwa falo itakuma ahankali Fatima tabude bayin ta shiga,  dayake yanzu tasan kan irin bayukan yan gayun nan sabida xaman lagos yasa ta kunna heater tafito ta kalli Amna tace "zomuje namiki wanka" dasauri ta tashi riganta tacire mata tana kokarin cire mata pant Granny tashigo rikeda kayan baccinta, sanan dawani kayan baccin a leda tamikama Fatima tace "ungo kema Mum dinki ta aikomiki da sabo" murmushi tayi ahankali sanan takarba tace "thank you" Granny tace "kina gama komi ki kashe wuta ki kwanta" gyadama Granny kai tayi ahankali, Granny tace "saida safen ku" atare suka mata saida safe, sanan tawuce bayi ta tahada ruwa tamata wanka da hadadden shower cream din dake bayin sanan suka fito ta shiryata cikin kayan baccinta ta kwantar da ita akan gado taja bargo tarufa mata ahankali tace "nima bari naje nayi" bayin tawuce tai nata wankan da ruwan zafi sosai tana karajin dadin jikinta sanan tadauro alwala tafito daga bathroom din tana kallon Amna dataga tai bacci, dan murmushi tasaki taje tabude kayan baccin, normal pj ne dogon wando da riga mai kamada t-shirt amman gajeren hannu yanad taushi sosai, hijabin dake kan sallayan tai tahau tai nafila sanan ta tashi ta linke dadduman takarasa takashe wutan saiga hasken wayanta dakuma ringing atare hakan yasa ta kalli screen din wayan dataga an rubuta Imam ajiki.

_Mumies akwai abinda nakeso nagaya muku, shin kunkosan like Did you know........?_
_Scent kamshi shine abu na farko da mutane ke lurada shi idan sun shiga gidan ka ko motan ka bawani abuba?_
_Be memorable.....in a good way Mumies_
 _A Fragrant, shi kamshi is like a signature, kaman wani alamune so even after a woman leaves the room, her fragrance should reveal she's been there. Kamshi abune dake nuna kinzo waje idan ma kikabar wajen still zai nuna kinzo_
_Turare heralds a woman's arrival and prolongs her departure_
_The beauty of turare speaks to your heart and hopefully someone else's kunsan da haka Mumies?_
_Kamshi is a word, turare is a literature do you believe this Mumies?_
 _Kamshinki amatsayin ki na y'a mace tells more about you sama da handwriting dinki kinsan da hakan?_
_Mata kusaurara kuji, namiji yana iya manta komi naki amman baya iya manta kamshin ki_
_da hakane nake muku introducing turarukan UMMIE COLLECTION dazai baki duka qualities dinan and even MORE tested by M SHAKUR dinku, suna saida turarukan daki, na jiki, na wanka, turarukan tsinke, body oils da sauran su, zaki iya tuntubar su ta wanan number ko awaya ko a watsapp 08186968736, dan samin karin bayani, zaku iyashiga group dinsu dan ganin duka turarukansu, zakuma ku iya following nasu a_ Instagram @UMMIE COLLECTION.

Open this link to join my WhatsApp Group:
https://chat.whatsapp.com/Fov2UbNr4CH0reP9K9zltu

Instagram Handle dinsu
https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1c3np4d6vwqbv&utm_content=1g4qyjp

_PRODUCT DINSU_
_SANDAL EXCLUSIVE_
_SANDAL FLAKES_
_SANDAL BANGI_
_KAJIJI_
_DOROT_
_DAMBU_
_DEVINE (PURPLE)_
_REGAL (YELLOW)
_LOVELY (MAROON)_
_DAISY (ORANGES)_
_KHuMRA_
_STAR_
_BELOVED_
_Body oils._

SIGN M SHAKUR

💫 _DISASTROUS LOVE_ 💫

✍🏾 M SHAKUR

EPISODE 5️⃣7️⃣

Saida gabanta yafadi dasauri takarasa gudun kar wayan yatada Amna tazare wayan daga chargy tama rasa mezatayi kawai tadaiga tai picking call din taga alamun yana kirga mata secs, ahankali takai wayan kunnenta tai hannunta nabari jin shiru yasa tacire wayan ta kalla ganin har lokacin call din nanan yasa takara kai wayan kunnenta ahankali tace "h......hello" tai maganan tana tashi ta kwanta akan gado ahankali tanajan bargo tana rufe kafanta, dan lumshe ido yayi yana gyara zama akujeranshi na office dan night yake, ahankali yace "Fatima" murya chan kasa kaman mai tsoron magana tace "uhm" saikuma tai shiru jin yayi shiru yasa ahankali tace "ina yini" ahankali shima yace "ya hanya? Kukai lafiya"? Murya chan kasa tace "lafiya lau" saikuma suka sakeyin shiru for so long hartana ciro wayan daga kunnenta ganin still call din is on yasa murya chan kasa tace "Thank you" ahankali taji yasauke ajiyan zuciya yace "for"? Alamun tambaya dan yanaso yasatai magana, only magana ne zaisa tasaki jikinta ta manta d past life dinta, murya chan ciki kaman tana tsoronshi tace "for bringing me to Baaba" tai shiru saikuma ahankali kaman tana shakkan fadi tace "and for giving me a family" murmushi yayi dahar saida taji sautin murmushin yace "you are welcome Fatima" suka sakeyin shiru saikuma chan yace "kinga Baffa na, da Mum da Amna" murya chan kasa tace "eh" saikuma chan tace "sunada kirki" dan murmushi yayi yace "ina Amna"? Ahankali tace "gatanan" murmushi yasakeyi yace "I guess kinyi sabon kawa kenan, saikin gaji da magana" dan murmushi kadan tayi dayasa yaji dadi dan yaji sound din murmushin, ahankali yace "take care, jeki kwanta" kaman yana ganinta

ta gyadamaikai sanan ahankali tace "nagode Ya Imam" lumshe idanu yayi sanan yabude su ahankali tareda katse wayan.

Janye wayan tayi daga kunenta ta ijiyeshi agefenta tajuya takife akatifa sabida hasken, sanan tai shiru tareda lumshe ido. "Ya To....bi" tafadi amugun hankali saikawai hawaye taji ya gangaromata daga idanu, tuna last ganinshi datayi jiyane sama sama yayi butu butu ya lalace kaman bashiba sama sama taga yana kuka yana jijjigata daganan batakara sanin inda kanta yakeba tadai tashi taga kanta a kano. Kife kanta tayi a filo tana kuka dabazama ta iya tantance namiye ba she is happy Allah yafitarda ita daga kangin wahalan nan nagidansu Tobi, yanzu she's back Allah yahadata da masu sonta but wani bangare na zuciyanta na wishing takoma gidan badan komiba saidan kawai taje taga Tobi, ayanda take ayanzu har cikin ranta jitake shikadai kawai zatagani taji she's fully happy. Kasa hakuri tayi tai kuka sosai sanan bacci yay nasaran kwaceta.

Karfe biyar daidai ringing wayar ya tadata harsaida ta firgita dan bata saba da wayaba, bama ta taba wayaba, daukan wayan tayi ganin Dr Imam ne yasa takara a kunnenta ahankali, cikin a very calm and light voice yace "tashi kiyi salla, lokaci yayi" murya chan kasa  tace "uhm" sanan yakatse wayan, ijiye wayan tayi ta tashi ahankali tareda kunna wuta ta kalli Amna yanda yarinyar ke diban bacci abinta tai lakur a bargo sanan tawuce tashiga brush tayi da komi tadauro alwala tafito daidai ana bude kofan dakinta Granny ce ganin tana fitowa daga bayi yasa tace "kin tashi Diyar kirki" gyadama Granny kai tayi, Granny dake rikeda da charbi tace "ok" xata juya tafita saikuma tadawo tace "namanta ban fadamiki ba banda tsarki da ruwan sanyi, ga bayi nan akwai ruwan zafi muddin akwai wuta kome kikayi kidinga tsarki da ruwan zafi kinji" ahankali tace "to" sanan takalli Amna dake baccinta sanan tawuce tafita tarufo mata kofa, hawa kan dadduma tayi tai rakatanil fajiri sanan tai sallan asubahi data idar tai azkar tai karatu sanan tashiga addiua Allah yacire mata kunci da damuwan datake ji aranta, wajajen 6:30 tagama komi tacire hijabi tafito tana sanye da kayan baccin dogon wando da riga peace sunmata kyau kanta nacikin hula tafito, kitchen din falon tashiga tadauko tsintsiya da paka tazo tabi falon nan tamai hadadden gyara sanan tabishi da mopping, showglass na turaren daks falon tabude tadauko turare da burner datagani ta kunna turaren sanan takashe komi datai amfani dashi tawuce kitchen saida tafara gyra kitchen din dabaiyi datti ba sanan tashiga store tana kalle kallen abinda zata dafa, wake tafara debowa ta wankesu tass ta jika aruwa sanan tadauko Irish tasami waje ta zauna tashiga ferewa kana ganinta kasan ba yarinya me kiwuya bace saida tagama sanan ta yayyanka, ta tashi tawuce tanika waken da attarugu da albasa a blender tasa ruwa kadan sabida karyay ruwa, tana gamawa tajuye a bowl sanan tasa mai aruwa tazuba Irish din itakuma takoma gefe tashiga bubbuga kosan, tanayin haka tana tashi idan Irish yasoyu ta kwashe tazuba a hadadden kula, bude kofan kitchen din akayi chak Granny ta tsaya tana kallon yanda tazauna kan wata yar karaman turmin dake kitchen din tana bubbuga kosai, salati tayi tace "oh ni yarsu waya saki aiki haka Zara keda yakamata ki koma bacci" murmushi tayi tace "dan Allah Granny karki hanani nizan dunga girki" dan jim Granny tayi saikuma tace "ai

